KUDI DA MACIJI (((1)))
Na :::::Nazir Adam Salihi:::::
A bakin wata katuwar fadama, da misalin karfe hudu da rabin wata ranar juma'a ta karshen karni na goma sha
takwas, wasu jinsin tsuntsaye suka yi sahu-sahu a bakin fadamar suna ta shakatawa abinsu domin kuwa
babu abin da ya dame su dan ba sa fargabar a fada musu da yaki, ko kuma a kawo musu hari kamar yadda
sauran jama'ar gari ke ta kwanan zulumin kasancewar wadannan abubuwa guda biyu a kansu.
Da yawa daga cikin tsuntsayen dake bakin fadamar neman abincinsu suke yi, yayin da wasunsu kuma ke ta
wanka abinsu, wasu ko sai shawagi suke yi a gefen fadamar suna kaiwa yan kananan kifaye hari ko Allah zai
sa su dace su sami abinci.
A can gefen fadamar daga yamma, wani manomi ya jefar da fartanyarsa gefe guda ya mike tsaye ya share
gumi, kana ya juya ya dubi matarsa wacce ke ta famar aiki babu ko sassautawa kai ka ce ita ce mijin.
"Ta Gogari." Mutumin ya kira sunanta cikin damuwa. Matar ta dago kai ta dubeshi a yatsine ta ce.
"To uban malalata yanzu fa sai ka ce har ka gaji ko? Na dauka tun da duku-dukun na zo gonar nan ban ce na
gaji ba sai kai da ka zo tsakar rana." Manomin ya dubi matar cikin murmushi.
"Haba ta Gogari, ke kin san ai na yi kokari ma da na kawo har ya yanzu ina noma, ni fa na rigaya na fada
miki ba zan iya noma ba, gara ki kyaleni akan sana'ata."
Ta Gogari ta dubi mijinta a fusace domin ta san abin da yake nufi.

"Oh! Amma dai Zangeru wallahi ka ji kunya yanzu ace mutum ya fifita sata akan sana'armu ta gado noma?"
Zangeru ya dubi ta gogari ya fashe da dariya. Sautin dariyarsa ya watsu a duk fadin fadamar harda dama
daga cikin tsuntsayen dake gurin suka tashi sama a tsorace.
"Haba ta gogari, kin manta da cewa abin da na gada kenan tun kaka da kakanni?" Ta gogari ta jefar da
fartaryar dake hannunta ta mike tsaye sosai ta dubeshi.
"Kai kasan da tunfarko na san kai barawo ne na rantse da Allah ba zan fara ma aurenka ba."
Zangeru ya sakato datti daga kogon kunnensa cikin murmushi ya ce.
"Kin ga kuwa ni a ganina wallahi duk cikin sa'anninki babu wacce ta yi dace da miji kamar ke domin ke kadai
ce kika yi dacen auren jarumi." Ta gogari ta turo baki gaba kamar suda.
"Wanene jarumin?" Zangeru ya bugi kirjinsa da karfi ya bada wani sauti fus! Tsuntsaye suka sake watsewa a
firgice ya dubi matarsa ta gogari ya ce.
"Ni ne jarumi, domin sana'ata bata rago ba ce."
"Ni kuwa a ganina babu rago kamar malalacin da ya zabi sata fiye da noma, dubi fa ciki ne da ni wata biyu
amma tun hudowar rana nake aiki har yanzu ban gajiya ba."
Zangeru ya kurawa matarsa ta gogari idanu na tsawon lokaci, sannan sai ya danki fartanyarsa ya rataya a
kafada ya ce.
"Shi yasa nake son ki rabu da wahala amma har kullum ina ta kokarin nuna miki Annabi kina runtse idanu.
Dubi cikinki ya fara girma, amma kullum kina kara cusa kanki cikin wahala." Ya dan yi shiru yana kallonta.
Ganin ta yi shiru ba ta ce komai ba sai ya ci

gaba.
"To ni yanzu ta gogari in banda abinki ma, dan abin nan da zamu samu a wannan yar gonar nawa yake? Shi
nan kanki ne a cikin dare guda ina iya tara miki abin da za mu yi shekara guda muna ci amma duk kin bi kin
dami kanki."
Ta gogari ta sunkuyar da kai tana murmushe kasar dake mammane a jikin busassun yan yatsunta wadanda
tsabar wahala da noma duk ya busar dasu kamar itace. Akwai alamun gajiyawa a fuskarta, kuma da yake
Zangeru ya kura mata idanu ya fahimci hakan. Wannan shi ya kara masa kwarin gwiwar cewa.
"Dauki fartanyarki mu tafi gida, kin ga rana ta tasamma faduwa." Ta gogari ta dago kai ta dubeshi ranta a
bace, ta bude baki kamar zata yi magana sai dai ta fasa ta dauki fartanyarta ta saba a kafada. Zangeru ya
dubeta da murmushi ya ce.
"Kwantar da hankalinki ta gogari nan da badi zan zama babban attajirin da ba a taba yin kamarsa ba duk
garinmu." Ta gogari bata ce dashi kala ba sai kawai ta bishi a baya suka nufi bakin fadamar nan wadda ga
al'ada a duk lokacin da suka zo noma anan suke dauraye jikinsu su sha ruwa kafin su koma gida.
Sa'ar da suka kai bakin koramar sai suka tsuguna suka fara dauraye jikinsu. Sassanyar iskar yammacin da ke
hurowa daga cikin fadamar ba karamin jefa Zangeru cikin nisnadi ta ke yi ba. Sau da yawa ya gwammace ya
wuni ya kwana gindin fadamar yana shan iska da lofe a hannunsa fiye da ace noma daidai da kunya biyu. A
daidai lokacin ne to ta gogari ta dubeshi ta ce.
"Na ji dazu kana yin wani mafalki wai kwanan nan zaka zama babban attajiri ko? Ta yaya to za

ka zama
attajirin? Da lalaci to ko da me?" Ta yi shiru tana
kallon mijinta Zangeru wanda ke zaune ya tura
kafafunsa
biyu cikin fadamar idanunsa lumshe yana
sauraren kukan tsuntsaye. Zangeru ya bude
idanunsa ya dubeta.
"Kina shakkar zamana attajirin ne?" ta gogari ta
yi dariya a karo na farko.
"Attajiri fa ka ce, ni ko na ga mutumin da bashi
son ko kankani ba shi son ya sha wahala a
rayuwarsa ta yaya
zai zama attajiri" Zangeru ya girgiza kai ya ce.
"Ta gogari kenan. Wato wani lokaci ki kan bani
mamaki da kike daukata a malalaci, kada fa ki
manta cewa
sana'ata ta fi karfin rago."
Kudi da Maciji... (2)
Ya dan yi shiru yana girgiza kafafunsa
akan ruwa akwai alamar murmushi a
bakinsa, duk kuwa da cewa bai fito fili ba
to amma Ta gogari ta lura da hakan. Sau
da yawa idan taga Zangeru yana irin
wannan boyayyen murmushi bata
magana domin duk sa'ar da zai fita wata
gawurtacciyar sata irin murmushin ya ke
yi.
"Sannu a hankali zan tabbatar miki da
zamana attajiri." Ta gogari ta sunkuyar da
kai ta ce "To Allah sawwaka."
Daga nan basu sake cewa da juna komai
ba sai ma'auratan biyu suka ci gaba da
wanke jikinsu. Tsahon lokaci suna cikin
wannan hali. Zangeru na cikin tsananin
nishadi, domin wani sa'ilin shi kadai sai ya
daki tsakiyar ruwa da kafarsa ya fashe da
dariya. Ta gogari bata tanka masa ba.
Daga inda Zangeru yake zaune yana iya
hango jerin sahu-sahun jinsin tsuntsayen
dake ta kai kawo suna shawagi a saman
fadamar kamar jirage. A cikinsu ne to
Zangeru ya lira da cewa akwai wata
balbela ita kadai tana tsaye a bakin

fadamar. Abin ya bashi mamaki domin duk cikin jinsin tsuntsayen ita kadaice bata da yar uwa. Balbelar ta taso a hankali cikin lalaci ta sauka a daf da inda su Zangeru suke zaune. Zangeru ya dubi balbelar cikin murmushi sannan ya dubi matarsa ya ce.
"Ta gogari dubi wata balbela mai kyau ta ziyarce mu." Ta gogari ta dubi balbelar shekeke, ta ce.
"Na ganta." Ta dauke kai gefe guda.
"Ya ya naga kin bata rai?" Ta gogari ta hade fuska ta ce.
"Haka dai ka iya, gashi nan yanzu ka rabomu da aikinmu ka kawo mu bakin fadama muna zaman banza, ka ga ni in ba yanzu za ka tafi ba ni ka barni in tafi gida ko kuma na koma gona na karasa sauran aikin dake gabana."
Zangeru ya dubi Ta gogari cikin murmushi kana ya dubi balbelar ya ce.
"Baki san irin yadda nake kaunar tsuntsaye bane musamman ma balbela shi yasa kike fadar haka. Dubi fa balbelar nan fara mai dogon wuya da jan baki kyakkyawa, kai ina ma ace, ina iya zama tsuntsu da na zama balbela." Ta gogari ta fashe da dariya ta ce.
"Oh! Zangeru al'amarinka sai kai." Zangeru ya dubi matarsa cikin nishadi ya ce.
"Allah kuwa Ta gogari da gaske na ke yi, domin ba ki ji yadda nake kaunar balbelar nan ba. Bari mu gani." yana fadin haka sai ya mika hannunsa zai kama balbelar. Ga mamakinsa sai kawai ya ga balbelar ta taso da kanta a hankali ya sauko akan cinyarsa. Nan da nan ya dubi Ta gogari cikin farin ciki.
"Kin ga abin da nake fada miki ko, ita ma balbelar ashe tana kaunata?" Ya dauki balbelar a hannunsa cikin tarairaya ya dubi Ta gogari.
"Ungo rike min da ita zan tafi gida." Ta

gogari ta mike tsaye ta dubeshi ta ce.
"Ka ga idan ba ka da aikin yi ni ina da shi a gida." Sai kawai ta juya zata fara tafiya. A daidai lokacin ne to suka ji kamar daga sama ance.
"Haba baiwar Allah, tunda ya ce dake ki rike masa ni yana kaunata ba sai ki daukeni din ba." Ta gogari ta tsaya cak kamar an soke ta da kibiya, ta juyo a razane, ko shakka ba ta yi ba Zangeru ne ke yi mata magana ba. Zangeru ya ji sautin muryar, shi kansa sai da abin ya sa shi mutuwar tsohuwa. Zaune a bakin fadamar numfashinsa ya dauke ya dubi balbelar cikin tsananin kaduwa ko shakka ba ya yi balbelar ce ke magana.
Ta gogari ta dubi Zangeru a tsorace ta ce bakinta na rawa.
"Wa...nene ke yi min magana...na ji muryar kamar ba kai ba?" Zangeru ya dubi balbelar dake kan cinyarsa cikin kaduwa sannan ya dubi Ta gogari.
"Ni ce nake yi miki magana baiwar Allah, gani na yi ya dage akan cewa yana kaunata ke kuma sai kokarin raba mu kike yi."
Ta gogari ta ja da baya cikin kaduwa ta ce.
"Ki yi min rai baiwar Allah ke kike ganinmu ba mu muke ganinki ba...wallahi ban san..." Ta gogari ta kasa karasawa saboda tsabar firgita.
"Kada ki ji tsorona domin ba zan taba cutar ki ba tun da mijinki ya ambata yana kaunata. Abinda nake so dake shi ne ki daukeni kamar yadda ya umarceki ku tafi dani gida domin daga yau har iya rayuwarku zaku kasance tare dani ba zaku taba rabuwa dani ba tun dai kuna kaunata." Zangeru ya yi ta yan mata ya tashi tsaye sai balbelar ta yi tsaye ta hau kan kafadarsa ta ce.
"Zo ki daukeni Ta gogari."
Ta gogari ta ji kamar an doke kafafunta

da gora, nan da nan ta ji juna biyun dake jikinta ya fara motsi kamar zata yi bari, tun kafin lokacin haihuwarsa ya karaso.

***

A daidai lokacin da duk wannan ke faruwa ne aka yiwa wani tsohon malamin gwanin iya bugun kasa iso a gidan sarki Sabitu. Wannan malami tsoho ne kwarai da gaske, kuma babu wanda ya san takamaiman shekarunsa a duniya domin duk garin babu ko da wanda ya kusan sa'a da shi. To amma duk da haka jita-jita na cewa tsohon zai yi kusan shekaru dari biyu zuwa dari biyu da hamsin a duniya. Kai akwai ma wani makaryacin baduku a garin da ya yi ta yada jita-jita cewar wai tsohon ya kai shekaru dari biyar har da tamanin. Wasu ko suna tunanin ma tsohon malamin ba mutum bane aljanne. To koma dai menene wannan tsohon malami mai suna Malam Dawaye shi ne babban malamin sarki Sabitu, kuma shi kansa sarki Sabitun ya gaji wannan malami ne a gurin mahaifinsa sarki mai kwarangwama.

IDAN NAGA ANA SO INSHA ALLAH GOBE ZAN CIGABA.

INNA FUSKANCI BA'ASO ZAN KYALE.

YAUWA.

Kudi da Maciji... (3)

Malam Dawaye dogone fari siriri sosai, ya tankware kamar baka, tun daga kansa har zuwa gemunsa babu alamar bakin gashi, sai fari tas! Kamar an shafa masa garin alli, to amma wani abin mamaki girar idonsa guda daya bangaren hagu baka ce sidik har tana kyalli, ko da yake wasu shakiyai sun ce wai bakin shuni yake shafa mata. Lokacin da wannan malami ya karaso gidan sarki la'asar sakaliya ce. Sarkin dogarai Hambara shi ne ya yi masa iso ya kuma wuce kai tsaye da shi har zuwa inda sarki Sabitu yake kwance, wanda yau kusan wata guda kenan yana

fama da matsanănciyar rashin lafiya.
Malam Dawaye ya durkusa gaban shimfidar sarki ya yi gaisuwa, sarkin dogarai ya amsa masa. Sannan sai sarkin dogaran ya mike tsaye zai fice daga dakin domin ya basu guri su gana. Sai sarki Sabitu ya dago kai daga kwance ya dubi sarkin dogarai sannan ya ce cikin shakakkiyar murya.
"Idan an yi sallar magariba ina son ka zo min da sarkin makera."
"An gama, Allah ya dada ma lafiya da imani."
Sarkin dogarai ya amsa sannan ya fice daga dakin cikin sauri. A zuciyarsa yana cewa anya kuwa sarkin nan ba mutuwa zai yi ba, domin ya fahimci kusan kullum a yan kwanakin nan sai sarki Sabitu ya gana da akalla aminansa guda uku zuwa hudu kuma duk a cikin sirri.
Ficewar sarkin dogarai ke da wuya sai malam Dawaye ya sake fadawa gaban sarki ya dada gaisuwa sannan ya ce.
"Allah karama lafiya da nasara gani." Sarki Sabitu ya dubi malam Dawaye daga kwance na tsahon lokaci. Akwai alamun karaya da sallamawa da duniya karara akan fuskarsa. Malam Dawaye ya fuskanci hakan, dan haka sai ya sunkuyar da kansa kasa, ba zai iya hada idanu da sarkin ba domin sai ya zubar da hawaye. Tsahon lokaci suna cikin wannan hali daga karshe dai sai sarki Sabitu ya ce.
"Malam Dawaye, abin da ya sa na kirawo ka shi ne na fahimci rashin lafiyar nan tawa ba ta tashi bace, kuma ba tun yau ba ka rigaya ka san irin muguwar kiyayyar da wazirina Danduna ke yi min, kasan kuma cewa babu makawa da zarar na mutu shi ne zai zama sarkinku." Ya dan yi shiru yana mayar da numfashi.
"Dawaye, a kullum na tuna da irin kiyayyar dake tsakanina da waziri Dandunawa sai na shiga cikin tsananin damuwa domin ban san irin halin da yan kananan yayana Hassan da Hussaina za su shiga ba. Wannan shi ne dalilin da yasa na kiraka domin ka buga min

kasa ka gano min irin yadda zasu kasance a hannun azzalumi waziri Dandunawa bayan mutuwa" Sarki Sabitu ya yi shiru, yayin da shi kuma Malam Dawaye ya shafi dogon gemunsa fari tas mai kamar gashin tunkiya, sannan ya janyo allon bugun kasar da ya zo da shi zuwa gabansa, ya baza shi da hannunsa sannan ya dubi sarki Sabitu ya ce.
"Allah ya baka nasara da lafiya an gama, bari mu gani ai wuyar aiki ba a fara ba." Fuskar sarki Sabitu ta washe kadan domin ya san tsohon malamin bai taba bugun kasa an sami wani kwakkwaran sabani ba. Domin a tarihi, a kuma iya tsahon lokacin da sarki Sabitu ya yi yana mulki, wannan tsohon malami ya buga masa kasa sau goma sha uku, inda duk ya tabbatar musu da samun nasarar yaki, amma sau daya tak a ka sami sabani inda suka yi kare jini biri jini, su da kudawa. Wannan shi ne yasa duk wani abu da ya shafi kasar tun daga hangen al'amuran da suka shafi yanayin gari zuwa albarkatun noma tsohon malamin ne ke bugawa ya sanar da sarki.
Malam Dawaye ya dubi allon dubar dake dauke da lallausan yashi, sannan ya fara zana alkaluman lissafi na duba yana gogewa, lokaci-lokaci sai ya daga kansa ya girgiza, sannan daga karshe sai ya dago kai ya dubi sarki ya ce.
"Allah baka lafiya da nasara, dabarar da kake kokarin yi ita ce kawai mafita kana son aikawa wani babban amininka dukiya mai yawa domin ya boyewa yayanka ko?" Sarki Sabitu ya gyada kai ya ce a tausashe.
"Tabbas, wannan shi ne nufina." Malam Dawaye ya ci gaba da cewa.
"Tabbas wannan dabara ce mai girma, domin a bayanka waziri Dandunawa tabbas shi zai zama sarki, kuma abin bakin ciki zai zamo daga cikin manyan azzaluman sarakan da ba a taba yinsu a kasar nan ba. Ina son kuma ka sani cewa da zarar ka mutu sarauta

zata bar hannun yan gidanku, za kuma a
cusgunawa yan gidanku, da yayanku guda
biyu Hassan da Hussaina wanda daga karshe
zai zamanto duk sun fice daga gidan
sarautar nan baki daya. Allah ya karama
nasara wannan shi ne abin da na gani."
Malam Dawaye ya yi shiru, lokaci guda kuma
ya sunkuyar da kai domin ya fahimci cewa
hawaye ne ke zuba kamar ruwa daga idanun
sarki Sabitu.
Shi kenan malam Dawaye, Allah ya hada
fuskokinmu a Darussalam." Sarki Sabitu ya
ce da shi. Malam Dawaye ya mike tsaye ga
mamakinsa sai ya ji hawaye ya kubuto daga
cikin idanunsa ya fara kwaranya akan
fuskarsa har zuwa cikin farin gemunsa.
Malam Dawaye ya sake duban sarki Sabitu
dake kwance, wanda tuni har ya rufe
idanunsa, ya kalleshi kallon da tuni jikinsa ya
bashi cewa me yiyuwa shi ne na karshe.
Sannan ya juya ya fice daga dakin.
Ficewar malam Dawaye ke da wuya sai ga
sarkin dogarai tare da sarkin makera sun
shigo, sarkin makera ya fadi gaban sarki
Sabitu ya yi gaisuwa.
Kudi da Maciji... (4)
Sarki Sabitu ya dubi sarkin makera mai masa ba
ya ce.
"Ina son nan da kwana uku ka keromin katuwar
akwati ta bakin karfe, wacce zata iya daukar
zinariya, lu-u lu-u da tagulla masu yawan gaske.
Ina kuma son ka yi mata hannaye masu karfin
gaske, wadanda idan an zo dora akwatin a bayan
doki ba za a sha wuya ba." Sarki Sabitu ya
saurara kadan yana mayar da numfashi, tuni har
idanunsa ya fara zubar da ruwa, gashi kuma
bakinsa sai rawa yake. Bayan ya dan huta sai ya
ci gaba.
"Ina son kuma ka yiwa akwatin manya-manyan
kwaduna guda shida, wadanda idan ba an yi
amfani da yayan makullayen kwadunan ba, duk
karfin mutum ka da ya iya budeta. Ina fatan zaka
iya?" Sarkin makera mai Masaba ya gyada kai

jikinsa na rawa.
"Allah ya dada ma nasara zan iya." Tun da ya ke rayuwarsa bai taba shiga dakin shakatawar sarki ba sai yau. To amma fa ba wai wannan bace ta sa jikinsa ke rawa. Zancen da ya ji na zinariya da lu'u-lu'u su suka fi tayar masa da hankali fiye da komai.
Domin duk da yake ya tabbata sarkinsu Sabitu mutum ne mai tarin dukiya, amma bai taba tsammanin yana da zinare da lu'u-lu'u da zasu cika katuwar akwatin bakin karfe ba. Sarkin dogarai ya ji bayan rigarsa ya fara jikewa da gumi, haka nan zuciyarsa na ta raya masa cewa ya kamata idan sun fita waje ya tambayi sarkin dogarai cikin hikima me yiyuwa ya tsurkunta masa dalilin da yasa sarki ake son ayi masu akwatin.
"Ina son ka yi mata hannaye wadanda idan na zo dora akwatin a bayan doki ba za a sha wuya ba..."
Kalaman sarki Sabitu ne ke kai kawo cikin kwakwalwar sarkin makera mai masaba. To wannan na nufin kenan dukiya ce sarkin ke nufin aikawa da ita wani guri. Wannan tunani shi ya dada sa jikin mai masaba ya dauki rawa kamar mazari.
"Nan da kwana uku nake son ka gama kirar akwatin, zan tura sarkin dogarai ya dauka."
Muryar sarki Sabitu ta sake dukan kunnen sarkin makera. Nan da na ya zabura ya dawo cikin hankalinsa, a zuciyarsa yana cewa. Irin wannan kuskure shi ke janyowa mutum yanka a gurin sarakai.
"Ranka ya dade an gama, in sha Allahu nan da kwana ukun zan gama."
Sarkin makera ya sake faduwa ya yi gaisuwa sannan ya fice daga dakin jikinsa na rawa. Ficewarsa ke da wuya sai sarki sabitu ya dubi sarkin dogarai ya ce.
"Ina son ka zabo min amintattu daga cikin mutanenka jarumai kamar mutum shida, ina son zan aike ku da wasu kaya zuwa gurin babban aminina, sarki Lurwanu." Sarkin dogarai ya

rankwafar da kai cikin biyayya, da girmamawa
sannan kuma da tausayawa. Ba tun yau ba ya
rigaya ya fahimci muguwar adawar dake tsakanin
sarkinsa sabitu da wazirinsa Dandunawa. Haka
nan ya riga ya san da yawa daga cikin fadawan
dake gidan sarautar duk Dandunawa suke goyawa
baya. Dan haka a yanzu da sarki ya ce da shi ya
samo amintattu daga cikin mutanensa bai yi
mamaki ba domin ya rigaya ya san cewa tun
sa'ar da tsohon sarkin ya fadi rashin lafiya goyon
bayansa ya raunana a gidan sarauta.
"Allah ya dade da ran sarki an gama." Sarkin
dogarai ya ce.
Wani zazzafan hawaye ya yi sartu akan kumatun
sarki Sabitu, sa'ar da ya dubi sarkin dogarai.
"Na gode da biyayya da kake yi min, na san kai
kadai ne ka rage mai kaunata daga cikin
mutanena, shi yasa nake son tattara dukiyata da
duk wani abu da na mallaka na daga gwala-
gwalai zinare, tagulla, da lu'u-lu'u, zan zuba su
cikin akwatin nan da na sa sarkin makera ya kera
min, za ku kai min ita gurin sarki Lurwanu, zan
hadaku da yayana Hassan da Hussaina ku tafi da
su can gurinsa, domin ni nasan tawa ta kare...ba
zan dada wasu kwanaki masu tsayi ba a
duniya..." Zuciyarsa ta karye ya fara shisshikar
kuka.
Sarkin dogarai ya yi sauri ya sunkuyar da kai
idanunsa cike da kwalla, tun da yake bai taba
ganin sarkinsa na zubar da hawaye ba ko da
kuwa barkono ne ya shigar masa idanu.
"Allah ya dada lafiya, kana iya dogara dani, in
Allah ya so zan isar ma da duk sakonninka a
gurin amininka sarki Lurwanu." Fuskar sarki
Sabitu ta dan saki, wani dan kankanin farin ciki
ya haskaka fuskar.
"Na gode, daman na san kai kadai ne zan iya
dogara da shi..."
Sarki Sabitu ya yi shiru a daidai lokaci da suka ji
wata zazzakar murya ta yi sallama a kofar dakin.
Ba a dade ba wasu kyawawan yara yan kimanin
shekaru goma sha hudu-hudu suka shigo cikin
dakin. Sarkin dogarai ya dubi Hassan da

Hussaina, cikin tsananin tausayi sai ya ji idanunsa sun ciko da kwalla. Mahaifiyar yaran ce ta fado masa a zuciya, yau kusan shekarunta goma sha hudu kenan da mutuwa, tana haifar yan biyun ta mutu. A zamanin da take raye ta taba bashi kyautar rigar saki. Sarkin dogarai ya sake kallon yaran sai ya ji wani dadai ya lullube zuciyarsa, a ransa ya fara fatan ina ma ace yayansa ne domin tun da yake bai taba haihuwa ba. Haka nan bai taba gajiya da kallon kyawawan yaran ba, musamman ma Hussaina tauraruwa mai kyawun duniya, kamar yadda wani mawakin sarki ya taba ce mata.
Yaran biyu suka shigo dakin, suka yi gaisuwa ga mahaifinsu sannan suka zauna akan kilishin da ya mamaye dakiin.
Kudi da Maciji... (5)
Sarki Sabitu ya yunkura daga kwance ya tashi zaune da kyar, ya dubi yaran biyu ya ce.
"Ga su nan sarkin dogarai na baka su amana a hannunka ka isar da su gurin aminina su da dukiyarsu, kada ka bari wani abu ya samesu, duk abin da ya samesu a hannunka!" Sarkin dogarai ya ce.
"Allah ya dada ma lafiya, babu wanda ya isa ya taba su in dai ina raye, har sai na isar da su."
Sarki Sabitu ya saki jikinsa gami da ajiyar zuciya sannan sai ya koma ya kwanta. A daidai lokacin ne to yarsa Hussaina ta dubeshi ta ce.
"Baba ina za a kai mu?" Sarki Sabitu ya dauke kai gefe guda domin ba zai iya hada idanu da ita ba, dan kada ta ga halin da yake ciki zuciyarta ta sosu.
"Gurin aminina sarki Lurwanu za a kai ku."
Hussaina ta dubeshi cikin mamaki ta ce."
"Baba a can zamu zauna ko za a dawo damu?"
Sarki Sabitu ya yi shiru na tsawon lokaci sannan sai ya ce.
"Me yiyuwa ku dawo...me zai hana watan wata rana kuna iya dawowa ai nan garinku ne."
Hawaye ya subuce masa.
***
Lokacin da sarkin makera mai masaba ya karasa

gida, sai ya kasa zaune ya kasa tsaye, haka nan daga ya zauna ya dan sarara sai ya ji kalmar. Zinare, lu'u-lu'u, tagulla na yawo cikin kwakwalwarsa. "Me ke damuna ne?" ya tambayi kansa da kansa.
Kusan sa'o'i biyu kenan da suka wuce yana faman sintiri daga kofar gida zuwa cikin gida. Tun sa'ar da ya dawo daga gidan sarkin, matarsa Habi ta dama masa fura kana ta shimfida masa tabarmar karauni kamar yadda ta saba yi ga al'ada, sannan ta fice zuwa makwabtansu dan yin ta'aziyyar mutuwa. Sarkin makera ya ci gaba da kai gwauro yana kai mari, sannu a hankali har sai da ya yi sawu goma sha biyar daga gidan zuwa tsakar gida sa'ar da ya dawo tsakar gidan ne to ya samu ya zauna akan tabarmar karaunin dake shimfide a tsakar gidan kusa da wani murhu mai dauke da wasu guma-guman duwatsu kan kura har guda uku.
Mai masaba ya dubi katon kokon wanda ke dauke da damammiyar fura, sannan ya dauke kai gefe guda, ya kurawa wani katon rumvu dake tsakar gidan idanu baya ko kiftawa.
Shekaru ashirin da suka wuce, sarkin makera bashi da wata sana'a da aka san shi da ita sai kira. To amma a boye a bayan kasa, ba shi da wata sana'a da ta wuce SATA.
Mai Masaba garsakeken kato ne, baki mai tarin gashin baki kamar ciyawa, hankanan yana da tarin gemu duguzumzum babu kyawun gani, sau da yawa idan ya dauki yan kananan yara da niyyar zai yi musu wasa sai su fashe da kuka idan suka dubi gemun, dan ya fi kama da abin tsoro fiye da gemu.
To amma duk da haka sa'ar da yana saurayi matarsa Habi tana mutuwar kaunarsa, a cewarta wai gemunsa shi ya fi burgeta fiye da komai a jikinsa.
Me yiyuwa matar tana da gaskiya, domin tun daga saman sa har zuwa sahunsa babu wani abin burgewa, domin komai a jikinsa babbane. Babban kai, faffadan kirji mai kamar kofar gari, manya-manyan tafukan hannu, wadanda ake jita-

jitar cewa wai ko doki ya mara da su sai ya
mutu.
Sarkin makera mai Masaba ya fara ne da turun barayi, domin tun yana saurayi yake karbar kayan sata ya sayar da su. Sannu a hankali har ya fara gawurta. Ran nan sai wani mutum mai shigen irin kirarsa ya same shi ya ce da shi.
"Ka ga mai masaba, ka daina batawa kan ka lokaci a banza. Domin wannan sana'ar kirar da ka sa a gaba ba wani attajiri zaka zama da ita ba, haka nan zaka yi ta zama kullum kana babbaka kirjinka a gaban wuta kamar fatar ganda, kuma ka ga turun barayin ma da ka ke yi ba wata riba mai yawa ke gare shi ba. Ni ina ganin ka shigo cikin mu kawai sai mu fara koya maka sana'armu ta dare..." tun daga wannan lokacin mai Masaba ya shiga cikinsu.
Wannan kusan shekaru ashirin kenan da wani abu, kuma har yanzun nan da yake zaune yana ta sakar zuci kamar gizo-gizo bashi da wata sana'ar da ta wuce SATA.
Dan haka a yanzu da mai Masaba ya zauna ya sa kokon furar a gaba, sai ya fara tuanin ko shakka babu ba zai iya samun saukin tunanin zuci ba har sai ya kaiwa babban abokinsa labarin katuwar akwatin da sarki ya sa a kera domin aikewa da lu'u-lu'u da zinare a cikinta. Har kullum babu abin dake damun mai Masaba sai ganin yau kusan shekarunsa ashirin da doriya yana sace-sace da fashe-fashe kamar bera amma har yanzu bai wuce a kira shi da matsiyaci ba. Tun da dai har yanzu jakinsa daya jal a duniya, bayan kuma ga makwabtansa nan attajirai ma'abota tarin dawakai dabbobi, da tumakai gami da tsuntsayen gida burjik, kullum miyarsu da mai da nama, amma shi kullum sai dai ya sha fura da tsantsaman nono! Wannan ba zata yiyu ba, ya dada jaddawa kansa. A daidai lokacin ne to ya tuna da kokon furar dake gabansa. Cikin lalaci mai masaba ya dauki ludayi ya kwarfo furar nan ya kai bakinsa ya dan kurba. Ga mamakinsa sai ya ji furar har wani daci-daci ta ke yi. Cikin sauri ya fesar da abin daya guntsa, sannan ya

mike tsaye a fusace.
"Gafara dai." Matarsa Habi ta shigo gidan da gafara dai, sannan sai ta yi turus tana kallon mijinta, lokaci guda kuma ta kalli kokon furar dake gabansa.
"Kada dai ka ce koma furar baka sha ba?" Habi ta tambayeshi. Gami da rike tsantsa.
Kudi da Maciji... (5)
Sarki Sabitu ya yunkura daga kwance ya tashi zaune da kyar, ya dubi yaran biyu ya ce.
"Ga su nan sarkin dogarai na baka su amana a hannunka ka isar da su gurin aminina su da dukiyarsu, kada ka bari wani abu ya samesu, duk abin da ya samesu a hannunka!" Sarkin dogarai ya ce.
"Allah ya dada ma lafiya, babu wanda ya isa ya taba su in dai ina raye, har sai na isar da su."
Sarki Sabitu ya saki jikinsa gami da ajiyar zuciya sannan sai ya koma ya kwanta. A daidai lokacin ne to yarsa Hussaina ta dubeshi ta ce.
"Baba ina za a kai mu?" Sarki Sabitu ya dauke kai gefe guda domin ba zai iya hada idanu da ita ba, dan kada ta ga halin da yake ciki zuciyarta ta sosu.
"Gurin aminina sarki Lurwanu za a kai ku."
Hussaina ta dubeshi cikin mamaki ta ce."
"Baba a can zamu zauna ko za a dawo damu?"
Sarki Sabitu ya yi shiru na tsawon lokaci sannan sai ya ce.
"Me yiyuwa ku dawo...me zai hana watan wata rana kuna iya dawowa ai nan garinku ne."
Hawaye ya subuce masa.
***
Lokacin da sarkin makera mai masaba ya karasa gida, sai ya kasa zaune ya kasa tsaye, haka nan daga ya zauna ya dan sarara sai ya ji kalmar. Zinare, lu'u-lu'u, tagulla na yawo cikin kwakwalwarsa. "Me ke damuna ne?" ya tambayi kansa da kansa.
Kusan sa'o'i biyu kenan da suka wuce yana faman sintiri daga kofar gida zuwa cikin gida. Tun sa'ar da ya dawo daga gidan sarkin, matarsa Habi ta dama masa fura kana ta shimfida masa

tabarmar karauni kamar yadda ta saba yi ga al'ada, sannan ta fice zuwa makwabtansu dan yin ta'aziyyar mutuwa. Sarkin makera ya ci gaba da kai gwauro yana kai mari, sannu a hankali har sai da ya yi sawu goma sha biyar daga gidan zuwa tsakar gida sa'ar da ya dawo tsakar gidan ne to ya samu ya zauna akan tabarmar karaunin dake shimfide a tsakar gidan kusa da wani murhu mai dauke da wasu guma-guman duwatsu kan kura har guda uku.
Mai masaba ya dubi katon kokon wanda ke dauke da damammiyar fura, sannan ya dauke kai gefe guda, ya kurawa wani katon rumvu dake tsakar gidan idanu baya ko kiftawa.
Shekaru ashirin da suka wuce, sarkin makera bashi da wata sana'a da aka san shi da ita sai kira. To amma a boye a bayan kasa, ba shi da wata sana'a da ta wuce SATA.
Mai Masaba garsakeken kato ne, baki mai tarin gashin baki kamar ciyawa, hankanan yana da tarin gemu duguzumzum babu kyawun gani, sau da yawa idan ya dauki yan kananan yara da niyyar zai yi musu wasa sai su fashe da kuka idan suka dubi gemun, dan ya fi kama da abin tsoro fiye da gemu.
To amma duk da haka sa'ar da yana saurayi matarsa Habi tana mutuwar kaunarsa, a cewarta wai gemunsa shi ya fi burgeta fiye da komai a jikinsa.
Me yiyuwa matar tana da gaskiya, domin tun daga saman sa har zuwa sahunsa babu wani abin burgewa, domin komai a jikinsa babbane. Babban kai, faffadan kirji mai kamar kofar gari, manya-manyan tafukan hannu, wadanda ake jita-jitar cewa wai ko doki ya mara da su sai ya mutu.
Sarkin makera mai Masaba ya fara ne da turun barayi, domin tun yana saurayi yake karbar kayan sata ya sayar da su. Sannu a hankali har ya fara gawurta. Ran nan sai wani mutum mai shigen irin kirarsa ya same shi ya ce da shi.
"Ka ga mai masaba, ka daina batawa kan ka lokaci a banza. Domin wannan sana'ar kirar da

ka sa a gaba ba wani attajiri zaka zama da ita ba, haka nan zaka yi ta zama kullum kana babbaka kirjinka a gaban wuta kamar fatar ganda, kuma ka ga turun barayin ma da ka ke yi ba wata riba mai yawa ke gare shi ba. Ni ina ganin ka shigo cikin mu kawai sai mu fara koya maka sana'armu ta dare..." tun daga wannan lokacin mai Masaba ya shiga cikinsu.
Wannan kusan shekaru ashirin kenan da wani abu, kuma har yanzun nan da yake zaune yana ta sakar zuci kamar gizo-gizo bashi da wata sana'ar da ta wuce SATA.
Dan haka a yanzu da mai Masaba ya zauna ya sa kokon furar a gaba, sai ya fara tuanin ko shakka babu ba zai iya samun saukin tunanin zuci ba har sai ya kaiwa babban abokinsa labarin katuwar akwatin da sarki ya sa a kera domin aikewa da lu'u-lu'u da zinare a cikinta. Har kullum babu abin dake damun mai Masaba sai ganin yau kusan shekarunsa ashirin da doriya yana sace-sace da fashe-fashe kamar bera amma har yanzu bai wuce a kira shi da matsiyaci ba. Tun da dai har yanzu jakinsa daya jal a duniya, bayan kuma ga makwabtansa nan attajirai ma'abota tarin dawakai dabbobi, da tumakai gami da tsuntsayen gida burjik, kullum miyarsu da mai da nama, amma shi kullum sai dai ya sha fura da tsantsaman nono! Wannan ba zata yiyu ba, ya dada jaddawa kansa. A daidai lokacin ne to ya tuna da kokon furar dake gabansa. Cikin lalaci mai masaba ya dauki ludayi ya kwarfo furar nan ya kai bakinsa ya dan kurba. Ga mamakinsa sai ya ji furar har wani daci-daci ta ke yi. Cikin sauri ya fesar da abin daya guntsa, sannan ya mike tsaye a fusace.
"Gafara dai." Matarsa Habi ta shigo gidan da gafara dai, sannan sai ta yi turus tana kallon mijinta, lokaci guda kuma ta kalli kokon furar dake gabansa.
"Kada dai ka ce koma furar baka sha ba?" Habi ta tambayeshi. Gami da rike tsantsa.
Kudi da Maciji... (6)
"Na fara sha sai na ji daci kamar kin watsa

shuwaka a ciki." Habi ta harareshi ta ce.
"Daci fa ka ce, ko kuwa dai bakinka ne yake dacin?" Sarkin makera mai masaba ya juya ya nufi kofa ba tare da ya sake dubanta ba.
"Ina kuma za ka?" Habi ta tambayeshi.
"Gidan babban aminina zani." Habi ta ji gabanta ya fadi ras! Domin ta rigaya ta san duk duniya mijin nata ba shi da wani amini da ya wuce tsohon barawon nan. Shekaru ashirin da suka wuce kullum a cikin fargabar rana zata bacewa mijinta take, to amma cikin sa'a ga shi dai har yanzu ko kai ba a taba fasa masa ba. Amma duk da haka Habi ta san ko ba dade ko ba jima watarana ba zata ga daidai ba. Dan haka a yanzu da ya ce za shi gurin amininsa sai ta ji fargabar da ta dade tana yi ta sake mamayar zuciyarta, dan ta san aminan biyu basu taba kulla abin arziki ba a tsakaninsu.
"Amininka wa kenan kake nufi?" Habi ta tambaya duk kuwa da cewa ta san wanda yake nufin.
Sarkin makera ya dubeta cikin murmushi ya ce.
"Kin fi kowa ai saninsa, ke kin san duk duniya bani da abokin da ya wuce ZANGERU!" yana fadin haka sai ya fice daga gidan cikin sauri. Matarsa Habi ta bishi da kallo cikin kaduwa. A daidai lokacin ne jakin sarkin makera ya fara wani mummunan kuka. "Uhu! U, wu! U!" Habi ta dubi jakin a fusace ta ce.
"Allah ya yi min tsari da kai la'ananne. Ta sha ji ana cewa duk sa'in da ka ji jaki yana kuka wai shaidani ya gani! Habi ta yi mamaki in jakin shaidanin ya gani yana bin mijinta a baya.
***
Zangeru na gaba dauke da fartanya matarsa ta gogari na bin sa a baya dauke da balbela zugum-zugum babu mai cewa kala kowa cikinsa ya duri ruwa kamar masu zuwa gidan makoki.
Ta gogari da kyar take tafiya, haka nan balbelar dake dauke a hannunta ta sa ji take yi kamar dauke take da maciji, domin ita duk gani take yi kamar balbelar za ta yi tsalle ta cakar mata idamu koma ta makureta. Idan har akwai abin da Ta gogari take tsoro bai wuce aljani ba. Sai gashi

yau da kanta ta dauko aljanar a hannunta za ta kaita har gida.
Zangeru kuwa wanda ke gaba yana jan kafa da kyar ji yake yi kamar an sa masa sasari a kafa. A iya tsayin zamanin da ya yi yana harkar sana'ar bera ya yi gamo da hadarurruka iri daban-daban, amma har zuwa wannan lokaci bai taba gamo da aljanu ba, domin shi a tunaninsa ma in banda ya ji ana ta fada, kuma wani malaminsa wanda ke biya masa karatun kur'ani tun yana karami ya taba yi masa bayanin wata aya da take magana akan aljanu, da sai Zangeru ya ce babu aljanu ma sam-sam a duniya tun da dai bai taba gamo da su ba. To sai gashi kuma yau da kansa ya daukowa kansa jaraba.
Sannu a hankali har su Zangeru suka karaso cikin gari. Sa'ar da suka shigo ta cikin babban dandalin garin sai mutane suka yi ta binsu da kallo cikin mamaki, domin abin mamaki ne ace mutum ya rasa abin da zai zo dashi gida daga gona sai balbela!
A daidai lokacin da suka karaso kofar gidan sarkin aska ne, sai matarsa wacce ta kasance kawace ga Ta gogari ta leko ta ce.
"Oh! Ta gogari yau kuma da balbela kuka zo mana daga gonar, hala wannan balbelar yar misirace?" Ta gogari ta dubi mijinta Zangeru sannan ta dubi matar sarkin aska da murmushin yake ta ce.
"Me yasa kika ce haka, ko gani kika yi kyawunta ya yi yawa" Matar sarkin aska ta girgiza kai ta ce.
"A'a, gani dai na yi duk balbelun dake cikin garin nan basu isheku ba har sai kun zo da wata daga daji."
A karo na farko sai Zangeru ya dubi matan biyu dake jayayya ya ce.
"Ku fa idan kuka fara jayayya kun yi ta yi kenan, da Allah Ta gogari taho mu karasa gida kada almuru ya riske mu a kofar gidan wanzamai."
Matar sarkin aska na jin haka sai ta fashe da dariya ta ce.
"A'a ha, Zangeru in dai yar sarautar nan tamu ce

kakewa bakin ciki bari kaima na baka sabuwar sarauta, daga yau na nadaka sarkin balbelu"! Suka fashe da dariya, sannan su Zangeru suka wuce.
Lokacin da su Zangeru suka karasa gida almuru ya rigaya yi, haka nan har yanzu cikinsu dure yake da ruwa domin basu san yadda za su yi da balbelar ba. A haka cikin tsananin fargaba suka shigo katuwar farfajiyar gidan, ma'abociyar shuke-shuken bishiyar zogale da kabewa. Daga bangaren kudu kuwa na gidan baka hango komai sai tarin ciyayi ko ina marasa amfani, haka nan daga bangaren gabas wata tsohuwar rumfa ce shekararriya wacce wasu awaki guda biyu ke karkashinta a daure. Su kansu awakin asalinsu Zangeru ne ya sato su a wani kauye dake makwabtaka da su. In ka dauke rumfar dabbobin fankadediyar farfajiyar gidan bata mallaki komai ba sai wasu bukkoki guda uku, da kuma wani tsohon rumbu, wanda rabonsa da ya dauki sama da damin gero biyar tun Zangeru yana dan saurayi.
Wadannan bukkoki guda uku da tsohon rumbun gami da awakin nan guda biyu na sata su kadai ne arzikin da zangeru ya mallaka a duk tsawon shekarun da ya yi yana sata. Sau da yawa Ta gogari ta sha nuna masa cewa shi fa zalunci ba abin yi bane, kuma bai sa mutum ya yi arziki, kuma koda ya yi arzikinma ba zai taba jin dadin arzikin ba, to amma sai Zangeru ya dubeta ya fashe da dariya ya ce.
Kudi da Maciji... (7)
"Ta gogari kenan! Ai idan kika ji ana cewa wai ba a arziki da kayan sata to daman satar ba ta kai sata ba." Wannan shi ya sa sa'ar da Zangeru ya sato awakin nan guda biyu sai ya ce da Ta gogari.
"Ga wadannan awakin ki ci gaba da kiwata min su da sannu zan samo musu yan uwa, domin lokaci ya yi da ya kamata na nuna miki cewa ana arziki da kayan sata, kuma akalla dai a yanzu ko da mutuwa nayi na san na barwa dan dana AMADI gadon awaki guda biyu."

Wannan Amadi da Zangeru yake magana akai shi
ne babban dansa kwaya daya jal a duniya.
Sabanin iyayensa, Amadi kyakkyawa ne dogo fari
mai dan siririn fashin goshi, zai kai kimanin
shekaru goma sha tara a duniya, tun daga kansa
mahaifiyarsa Ta gogari bata sake yin ko batan
wata ba sai a wannan karon da ta sami ciki
akalla wata takwas.
Sabanin mahaifinsa Amadi ba shi da wani aiki da
ya wuce farauta wata sa'ar idan ya fita farauta
sai ya yi wata guda bai dawo ba.
Dan haka sa'ar da mahaifan Amadi Zangeru da
Ta gogari suka karaso farfajiyar gidan dauke da
balbelar sababin sai suka yi mamakin ganin
kayan farautar Amadi, gami da wasu zomaye
guda shida yankakku da beguwa biyu da damo
biyar duk zube a tsakar gidan.
Zangeru ya dubi kayan farautar, sannan sai ya
jefar da fartanyarsa ya zauna jagwab a gaban
kayan farautar. Ta gogari ta yi sauri ta zauna
kusa dashi sannan bakinta na rawa sai ta mika
masa balbelar ta ce.
"Ungo balbelar ka." Zangeru ya dubi Ta gogari a
tsorace, jikinsa na rawa kamar mazari, ya mika
hannu ya karbi balbelar yana mai addu'ar Allah
ya kawo dansa Amadi ko sa sami mafita, domin
ya san duk inda Amadi yake bai yi nisa ba tun da
dai ga kayansa nan ya dawo.
Kudi da Maciji... (8)
"Ki saki jikinki dani baiwar Allah ni mai
kaunarku ce sannu a hankali za ku saba dani
kamar yadda kuka saba da dan kyakkyawan
yaran nan naku Amadi mafarauci."
Ma'auratan biyu suka dubi juna cikin
tsananin mamaki da kaduwa. Zangeru ya
dubi balbelar cikin kaduwa ya ce.
"A...ina kika san Amadi?" Balbelar ta karkada
fukafukanta biyu ta ce.
"Mun sha haduwa dashi a cikin daji inda yake
farauta, tun yana karami nake ganinsa, shi
ne dai bai sanni ba." Balbelar ta dan yi shiru
sannan sai ta dubi namun dajin dake zube a
tsakar gidan ta ce.

"Ko jiya ma a gabana ya kashe wadannan zomayen guda biyu." Balbelar na gama fadin haka sai ta yi tsalle sama ta sake direwa, sannan sai ta yi girgiza da karfi. Nan da nan wata bakar guguwa ta turnuke gurin. Ta gogari ta tashi a tsorace ta nufi inda maigidanta Zangeru yake ta fada akan cinyarsa ta kankame shi cikin razana.
"Kada ku tsorata, ba wani abu zan yi muku ba Ai ni da ku alkawari ne babu cuta ko cin amana."
Wata siririyar murya ce ke fadin hakan. Ba a dade ba sai guguwar ta tsaya cak.
Ma'auratan biyu suka yi ajiyar zuciya, kana suka dubi inda balbelar take. Har yanzu tana nan tsaye, sai dai kuma wannan karon Balbelar dauke take da wani dan madaidaicin dutsen kankara fari sol a bakinta. Balbelar ta yi tsalle ta sauka a kafadar Zangeru, sannan ta saki farin dutsen ya fado tsakanin cinyoyinsa. Ta gogari ta dada kankame Zangeru a tsorace, ji take yi kamar zata sume.
Balbelar ta dubi farin dutsen ta ce da Zangeru.
"Dauki farin dutsen nan ka adana shi, duk sa'ar da kake bukatar wani taimako daga gareni, jefa dutsen kawai zaka yi a bakinka, ko kuma ka murza shi tsakanin tafin hannayenka zan bayyana." Balbelar ta yi tsalle ta baro kan kafadar Zangeru ta sake direwa a kasa sannan ta ce.
"Ni zan tafi sai kun bukaci ganina kuma!" tana fadin haka sai ta tashi firrr! Ta tafi abinta.
Zangeru da Ta gogari suka bi balbelar da kallo cikin kaduwa, har sai da ta bace a sararin samaniya sannan suka yi ajiyar zuciya baki daya.
Ta gogari ta yi sauri ta bar jikin mijinta ta zauna a kusa dashi, sannan ta dube shi jikinta na rawa ta ce.
"Ga irinta nan ai, lalacinka da shisshiginka ya

janyo mana bakar jaraba har gida!" Zangeru ya dauki dan farin dutsen da balbelar ta bashi ya juya shi a hannunsa sannan ya dubi Ta gogari cikin murmushi ya ce.
"Idan kika kara zaginta, sai na murza dutsen nan na ta dawo miki yanzu-yanzun nan!" Ta gogari ta ja da baya a tsorace.
"Ka rufa min asiri don Allah Zangeru. Wai me ke damunka ne? Kai yanzu har ma fatan ka sake ganinta kake yi? Ni Wallahi da zaka biya ta tawa ma da sai ka jefa datsen nan cikin rijiya, ka ga mun rabu da ita kenan har abada."
Zangeru ya saki wani busasshen murmushi kana ya dada duban dutsen dake hannunsa ya ce.
"Kin cika yanke hukunci da wurwuri Ta gogari, kika sani ko wata rana zamu bukaci taimakon nata?"
A daidai lokacin da duk wannan ke faruwa ne to Amadi ya shigo gidan dauke da kwari da baka.
Mahaifan nasa suka yi shiru lokaci guda sannan suka zuba masa idanu.
"Lafiya na ga duk kun yi jugum-jugum?" Zangeru ya yi sauri ya saki murmushin yake ya ce.
"Lafiya lau Amadi, Dawowarmu kenan daga gona. Ina fatan ka dawo lafiya?" Amadi ya ajiye kwari da bakarsa a gefe guda sannan ya dubi mahaifiyarsa ya ce.
"Lafiya lau, amma ina jin gobe ma zan koma, daman zuwa na yi na kawo muku wannan." Ya nuna zomaye da sauran naman farautar dake zube a tsakar gidan.
"An gode Amadi Allah ya saka ma. Bari ma in tashi na gyarasu." Ta gogari ke fadin haka lokaci guda kuma ta mike tsaye ta nufi inda yankakkun zomayen suke. Ta gogari na durkusawa akan zomayen kenan sai suka ji kamar daga sama wata gargajejiyar murya ta ce.
"Gafaranku dai masu gidan nan!" Ta gogari

ta juyo cikin sauri ta dubi kofar gidan. Nan da nan ta ji yawun bakinta ya kafe, bugun zuciyarta ya dadu.
Ko daman kafin ma ta juyo ta san duk duniya babu mai wannan gwarjejiyar murya mai kamar goge sai mutum daya, mutumin da ya kasance babban amini ga maigidanta amma har yau bata taba farin ciki da ganinsa ba, domin Ta gogari ta rigaya ta san mutumin tauraruwa mai wutsiya ne ganinsa ba alheri ba. Mutumin dogo baki mai katon kai da tarin gashin baki da bujujun gemu gami da faffadan kirji kamar kofar gari ya matso kusa da su ya dubi Zangeru da faffadan murmushi yace.
"Tun a hanya nake ta addu'ar Allah sa na sameka." Ya dan yi shiru "Tashi mu fita daga kofar gida, wani labarine ke cina, shi ne na zo maka da shi tun da dumi-duminsa."
Zangeru ya mike cikin sakin fuskarsa a washe ya ce.
"Sarkin makeran duniya, MAI MASABA, ni daman na san ai ungulu bata jewar banza. Da me ka zo mana?" Mai masaba ya dubi Amadi da Ta gogari sannan sai ya kiftawa Zangeru idanu ya ce.
"Zo mu fita daga waje." Zangeru ya bishi cikin sauri suka zagaya bayan danga. Ta gogari ta dubi Amadi cikin kunan rai, shi ko Amadi ya dubeta cikin mamaki ya ce da ita cikin rada.
"Wai daman har yanzu BABA bai daina muguwar sana'ar nan ba?"
Kudi Da Miciji
Part 9
Tagori ta ji kamar hawaye zai zubo mata dan haka sai ta dauke kai gefe guda ta ce.
"Me hali ai baya barin halinsa Amadi."
***
Ina jin fa ga dukkan alamu Zangeru, tsuntsu daga sama gasasshe na kokarin fadowa a cikin akushin mu." Mai masaba ya ce da Zangeru sa'ar da suka zauna akan ciyawar da ta mamaye jikin

dangar gidan suka mike kafafunsu kamar masu daukar darasu. Daga inda jibga-jibgan mutanen guda biyu suke, suna iya hango wata katuwar duhuwa ma'abociyar yawan bishiyoyi da ciyayi, haka nan a daf da duhuwar wasu jakai ne guda biyu da shanu guda uku suna kiwo abinsu suna harbin iska babu abin da ya damesu a duniya.
Zangeru ya muskuta ya lalubi katon goro ya bara shi gida biyu ya jefa rabi abakinsa sannan ya mikawa mai Masaba rabin sannan ya dada da cewa.
"Bani labari na sha abokina, me ka gano mana?"
Mai masaba ya jefa bangwalelen goron mai kamar kataura gaba daya cikin bakinsa ya fara taunawa rumus-rumus kamar jaki na cin danyar ciyawa.
Dazu-dazun nan na dawo daga gidan sarki, an umarceni da na kera wata katuwar akwatin karfe."
Mai masaba ya yi shiru yana duban fuskar Zangeru.
Zangeru ya daga hannu cikin kosawa ya ce.
"To ci gaba mana ina sauraronka, an kira ka gidan sarki an ce ka kero katuwar akwati uhm-hum."
Mai masaba ya zura hannunsa baya ya karyo wani dan siririn kara daga jikin dangar ya fara sosa doron wuyansa da karan. Duk abin da yake yi Zangeru na kallonsa ya lura akwai alamun damuwa karara a fuskar mai Masaba.
"Abin ne yana da matukar hadari, domin idan muka yi kuskure ko da kankanine zamu iya hasarar rayuwarmu, idan kuwa muka yi nasara, mun gama shiga sahun attajirai kenan, domin ba su ba har tattaba kunnenmu sun rabu da talauci, me yiyuwa ma dole ne mu bar garin."
Zangeru ya shura kafafusa biyu cikin rairayi sa'annan ya dubi mai masaba cikin kaguwa da damuwa.
"Ni har yanzu na kasa fahimtar inda soki burutsun nan naka ya sa gaba, ya kamata ka warware min zare da abawa." Mai masaba ya yi ajiyar zuciya ya ce.

"Wato wannan katuwar akwatin karfe da nake baka labarin ansa ni na kera, sarki Sabitu ne ke son kwashe duk wasu ma'adinai masu daraja da ya mallaka zai aike dasu zuwa gurin babban amininsa Sarki Lurwanu." Zangeru ya saki wani kwakkwaran huci, rairayin dake gabansa ya yi sama fu!! Kamar yar karamar guguwa.
"Ma'adanan da kake magana a kai suturu ne ko makamai ko kuwa me?" mai Masaba ya saki wata kekasasshiyar dariya.
"Wata sa'ar Zangeru na kan dade ban ga shashasha kamar ka ba, in banda abinka akan wasu suturu ko makamai karafan banza zan dauko kafa na biyo ka har gida dan kawai jin dadin hira? To bari ka ji ina son ka bude kunnuwanka da kyau, wannan akwatin da nake baka labari cikata za a yi da gwala-gwalai, zinare da lu'u-lu'u!" Zangeru ya zabura cikin kaduwa nmfashinsa ya dauke.
"Ba ka da hankalimai Masaba, Lu'u-lu'u fa ka ce cikin akwati!" Mai Masaba ya yiwa Zangeru murmushin yake ya ce "kada ka yi shakkar duk abin da na fada maka."
"To kai duk a gurin wa ka sami wannan labarin, kada ka samu wahalar banza, na san dai nufinka shi ne mu tare wanda sarkin zai aika muyi fashin akwatin ko ba haka kake nufi ba?" Mai Masaba ya fashe da dariya ya ce.
"Dadina da kai saurin fahimtar zance da inda zancen ya nufa." Mai Masaba ya dan yi shiru sannan sai ya dubi Zangeru ya ci gaba.
"Ka san sarkin dogarai tsohon abokina ne, a gurinsa duk na sami labarin, dan shi ne shugaban ma wadanda za a aika da kayan a cewarsa su shida za su raka akwatin kayan."
"Shu Shida!" Zangeru ya tambaya. Mai masaba ya gyada kai.
"Ka ga kenan in har muna son mu ji dadin yi musu kofar rago muna bukatar karin mutum daya kenan, kaga kowane daya daga cikinmu sai ya yi maganin mutum biyu daga cikin fadawan kenan." Mai Masaba ya gyada kai cikin gamsuwa.
"Kwarai kuwa muna bukatar karin mutum daya,

amma ina jin ai MAKWARO naka yana gari ko?"
Zangeru ya dan yi kasake yana tunani can sai ya gyada kai ya ce.
"Kwarai kuwa muna iya tafiya da Makwaro, kasan kuwa gwanine wajen iya harbi dan banza da katon kai kamar murhu." Mutanen biyu suka fashe da dariya sannan suka mike tsaye lokaci guda Zangeru ya dubi Mai Masaba.
"Yaushe ne ranar da za su yi tafiya?" Mai masaba ya shafi keya.
"Wannan shi ne ban sani ba, yanzundai kwana uku aka bani na gama kirar akwatin, na san kuma sarkin dogarai ne zai zo daukar akwatin, zan yi kokarin na bugi cikinsa na ji ranar da za su fita da kuma ta hanyar da za su bi. Domin yanzun zuwa dai na yi na tsurkunta maka dan ka zama cikin shiri."
"Kada ka ji komai" Zangeru ya ce, cikin gaggawa.
"Ni daman kullum a shirye nake, wanda ke neman kuka ballantana aka jefe shi da kashin awaki ni daman fa wallahi Mai masaba, na gaji da kanana-kanan sace-sacen nan, kullum fatana shi ne na yi katuwar satar da zan zama attajiri kaga daga nan sai na tuba na bar sata." Mai masaba ya fashe da dariya ya ce.
"Lallai abokina ko yaushe tunanina iri daya ne da naka."
Mutanen biyu suka fara tafiya a hankali suka bi yar siririyar hanyar da zata kai su har can cikin gari....
Kudi da Maciji... (10)
Koda suka fara tafiya sai Zangeru ya dubi mai masaba ya ce.
"Idan mun yi nasara ya ya zamu yi da wannan tarin dukiya? Mai Masaba ya dan yi shiru yana girgiza kai sannan sai ya ce.
"Lallai ka zo da babbar tambaya, amma yanzu dai bari mu fara samun dukiyar tukun, samunta ya fi yadda za ayi da ita wuya, idan muka yi nasara ba sai mu bar garin ba me kuma zai kara zaunar da mu a wannan garin, gara mu tafi can nesa inda za mu sha gararin gabanmu cikin nutsuwa ai KUDI DA MACIJI

MAGANINSU KASHEWA Zangeru."
Sa'ar da mutanen biyu suka zo rabuwa, sai suka yi musabiha da juna, kai ka dauka wasu shehunan malamai ne. A lokacin ne to Zangeru ya dubi Mai Masaba ya ce.
"Yanzu sai yaushe kenan zaka zo mu yi shirin karshe?"
"Da zarar na kai akwatin, na kuma bugi cikin sarkin dogarai zan dawo. Kai dai sai ka yi kokarin ka sanar da MAKWARO ya zama cikin shiri." Mai masaba ya na gama fadin haka sai ya juya cikin sauri ya bar Zangeru tsaye. Zangeru na na tsaye yana kallon bayan amininsa Mai Masaba, har sai da ya bace a cikin duhun almurun. Zangeru ya juya ya nufi gida zuciyarsa na ta sake-sake. Koda ya fara tafiya, sai ya tuna da farin dutsen dake daure a gefen bantensa. Balbelar ta fado masa a rai. Ga mamakin Zangeru sai ya ji hannunsa ya kai ga dutsen. Zangeru ya mulmula dutsen da yan yatsunsa sannan sai ya yiwa kansa murmushi.
"Anya kuwa lokacin da zan bukaci taimakon balbelar bai zo ba?" zangeru ya tambayi kansa, sa'ar da ya sake mulmula dutsen.
***
Washegari da la'asar sakaliya Gimbiya Hussaina yar sarki Sabitu ta yi hawa ita da wasu amintattun kuyangin sarki Sabitu shida, suka nufi wani makeken gandun sarkin wanda ke dab da katuwar koramar nan ta Dan masu. Wannan shi ne karo na farko da Hussaina ta fita irin wannan kilisa ta shakatawa tun bayan da mahaifinta sarki Sabitu ya kwanta rashin lafiya.
"Kada ku takurawa kanku akan rashin lafiyata, ku tafi ganduna ku shakata ko kwa sami saukin damuwa." Sarki Sabitu ne ke cewa yayan nasa biyu a safiyar ranar domin ya fuskanci tun bayan da ya kwanta rashin lafiya bai kara ganin su cikin walwala ba. Wannan shi yasa Hussaina hawa ita da kuyanginta, duk kuwa da cewa Hassan na

can tare da mahaifinsa bai yarda ya bisu ba. Lokacin da Gimbiya Hussaina da kuyanginta suka karaso cikin ni'imtaccen gandun, sai suka tarar tuni har bayin sarki sun kafa musu wata katuwar rumfa ta alfarma an shimfide cikinta da tausasan kilisai da matasan kai da fitilu masu hasken gaske domin ga ala'ada sukan kai har dare wata sa'ar basu koma gida ba. Wasu kuyangi guda biyu masu dan siririn wuya kamar na barewa suka akamawa Gimbiya Hussaina ta sauko daga kan dokinta. Tana sauka sai duk farfajiyar ta game da kamshin dake tashi daga jikinta. Cikin takama fuskarta na annuri ta nufi cikin rumfar ta cire katuwar alkyabbar dake jikinta sannan sai ta dubi kuyangin ta ce.
"Bari in gangara cikin fadamar can na yi wanka, ku shirya mana kayan sha na dangin zaki, kafin na dawo." Kuyangin suka amsa cikin girmamawa.
Gimbiya Hussaina ta nufi katuwar fadamar ma'abociyar sansanyar iska, da tarin tsuntsaye. Tun daga nesa Hussaina ta ji sanyi ya fara bugun fuskarta, ga mamakinta sai ta ji duk da muguwar rashin lafiyar mahaifin nata, ranta ya yi fari tas, musamman da ta jiyo tsuntsaye sai rera wakoki suke yi cikin muryoyi iri daban-daban.
Wannan katuwar fadamar ni'ima da Hussaina ta nufa, tana da girman gaske, kuma wani dan karamin bangare nata ya shigo ta cikin gandun sarki sabitu sau da yawa ma da ruwan koramar ne fadawa suke ban ruwan shuke-shuken kayan zakin dake gandun na sarki. Dan haka a yanzu da Hussaina ta yiwa koramar tsinke, sai ta dinga bin gefen koramar da ya fara tun daga cikin gandun sarkin har zuwa waje.
Sannu a hankali Hussaina na tafiya a gefen fadamar, kyawawan kafafunta na fantsamar da ruwa a cikin ciyayin dake gefen koramar, har dai ta kawo dai dai wata yar duhuwar

dogayen ciyayi wanda daga sune Hussaina
zata riski inda take so ta yi wankan, domin
duk sa'ar da ta zo gandun anan take wanka
ba dan komai ba kuwa sai don dalilai guda
uku. Na farko dai ruwan dake dab da
wannnan dogayen ciyayi tsabtataccene, na
biyu kuwa ruwan ba shi da zurfi a wannan
bangaren, babban dalilinta na uku kuwa shi
ne gurin yana da matukar sirri, domin
dogayen ciyayin sun zagaye bakin ruwan
sunyi masa dan karamin kuri, wanda in tana
wanka a gurin babu wani mahaluki dake
wucewa ta kusa da koramar da ya isa ya
hangota, sai dai in ya kusanci gurin sosai.
Wannan kuwa bai cika damun Hussaina ba,
domin har kullum idan ta zo wanka ta kan
ajiye kayanta ne a gabar koramar kusa da
inda zata iya daukarsu cikin sauri, ya Allah
koda za ta jiyo motsin zuwan wani.
Lokacin da Hussaina ta kawo dab da wannan
ciyayi ne to ta ji wani kwakkwaran motsi a
cikin ciyayin, Hussaina ta tsaya turus, ta ji
kirjinta ya harba to amma bata tsorata sosai
ba domin ta riga ta san babu wani abu mai
hadari tattare da koramar to amma da yake
tun da take zuwa koramar bata taba jin
motsin komai ba sai ya sata faduwar gaba.
Kudi da Maciji... (11)
Hussaina ta ayyana a ranta cewa motsin ya fi
kama da na wani abu mai girma.
"Me yiyuwa wani dan karamin naman daji ne."
Hussaina tace cikin zuciyarta
tsawon lokaci Hussaina na tsaye cak a boye a
bayan ciyayin ita bata yi gaba ba, ita ko bata yi
baya ba shiru-shiru ba a sake motsin ba, jin haka
sai Hussaina ta saki wani tattausan murmushi.
"Hussaina yar budurwa kin cika tsoro, kamar ba
yar sarki ba." Ta ce da kanta. Sannan cikin
takama da tabbacin babu kowa a gurin ta turar
da dogayen ciyayin ta nufi bakin koramar. Tana
shiga tsakanin ciyayin ne to ta hango shi zaune
akan wani dutse da ta saba zama ta tsame
ruwan dake jikinta a duk lokacin da ta zo wanka

bakin koramar. Hussaina ta yi turus tsakanin ciyayin zuciyarta na harbawa tsakanin hakarkarinta domin a zuciyarta ta dauka aljanine. Saurayin dake zaune akan dutse dogone fari kyakkyawan gaske na gani a fadawa sarki, saurayin yana dauke da wani dan siririn fashin goshi. Haka nan dauke yake da wani kyakkyawan kanari ahanunsa.
Matasan biyu suka kurawa juna idanu na dan lokaci. Hussaina ta ji zuciyarta ta dulmiya, cikin sauri ta sunkuyar da kanta a tsorace bata iya ci gaba da kallonsa ba.
"Kai amma fa wannan saurayin ko aljanine da kyawu yake zita!" Hussaina ta ce cikin ranta. Ga mamakinta sai ta ji nan da nan tsoron dake zuciyarta ya gushe, sannan shaukin ta sake ganin kyakkyawar fuskar ya maye gurbin wajen. A hankali sai Hussaina ta sake dago kai domin ta sake kallon fuskarsa. Tana dago kai sai saurayin ya yi mata murmushi. Sannan ga mamakin Hussaina sai ta ji saurayin ya ce cikin wata tattausar murya.
"Ki yi hakuri ranki ya dade, ga dukkan alamu na tsorata ki ko?" Hussaina ta dada kallon kyakkyawan saurayin, batare da ta shirya ba sai ta ji murmushi ya subuce mata, lokaci guda kuma ta girgiza kai ta ce masa.
"Uhm-Uhm...ai ba wani tsorata sosai na yi ba...kawai dai ban taba tsammanin ganinka a nan bane."
Dogon saurayin ya mike tsaye akan dutsen, kana ya gyarawa kanarin dake hannunsa riko ya ce.
"Ni ma tsautsayine ya kawoni ranki ya dade, wannan tsuntsun dake hannuna shi na biyo, da kyar na kama shi."
Gimbiya Hussaina ta yi shiru tana sauraron saurayin. Akwai wani amo da muryarsa ke yi wanda yake burgeta.
"Idan kin yi min izini ranki ya dade ni zan tafi daman abin da ya kawoni kenan kuma na kamashi."
Ya dada nuna mata kanarin. Hussaina ta yi sauri ta girgiza kai.

"Kada ka damu, ni baka yi min laifin komai ba."
Ta dan yi shiru tana dubansa.
"Na gode ranki ya dade, Allah ya karawa sarki lafiya." Hussaina ta dube shi cikin mamaki ta ce.
"Anan garin kake ne?" Saurayin ya gyada kai.
"Ni talakanki ne ranki ya dade, gidanmu na nan daga karshen gari mahaifina...manomi ne." Ya ce da ita bakinsa na rawa.
"Amma kuma ban taba ganinka ba?" Hussaina ta tambaye shi cikin mamaki.
"Ai ban cika zama agida ba, wani lokacin ma sai na yi wata guda ko fiye da haka bana gari....ni mafaraucine kusan duk rayuwata a cikin daji take."
Jin haka sai ya burge Gimbiya Hussaina, dan haka cikin sauri sai ta dago kanta ta yi masa kallon girmamawa ta ce.
"Lallai ka isa jarumi...ni kuwa babu abin da na fi so a duniya kamar jarumi." Ta dan yi shiru sannan sai ta matsa dab da dutsen da yake tsaye ta dubeshi da tattausan murmushi.
Dan saurayin yayi sauri ya sunkuyar da kansa kasa sa'ar da ta matso dab dashi, haka nan kwarjininta duk ya daddaure masa jijiyoyin jiki, to amma duk da haka ya yi matukar jin dadin yabon da ta yi masa na jarumi.
"Yaya ka yi shiru, ai gara ka sauko daga kan dutsen ko, ko kuwa kafi son ka yi ta tsayuwa akai?"
Jikinsa na rawa saurayin ya sauko daga kan dutsen ya tsaya a gaban gimbiya Hussaina kanarin rumgume a kirjinsa. Wata sassanyar iska ta huro daga cikin fadamar ta fara fifita matasan biyu saurayin ya ji wani ni'imtaccen kamshi ya bugi hancinsa. Matasan biyu suka kurawa juna idanu na tsawon lokaci, suna kallon bambancin ajin dake tsakaninsu na yar sarki da dan talaka, haka nan zuciyoyinsu na masu fargabar rikicin da suke kokarin jefa kansu.
Hussaina ce ta fara ajiyar zuciya ta dube shi ta ce.
"Amma kanarin nan naka na da kyau, ban taba ganin irinsa ba." Saurayin ya yi mata murmushin

yake.
"Ko kina sonsa ne?" Hussaina ta gyada kai da murmushi.
"Na dade ina son na yi kiwonsa a gida, da za ka bani shi da na fansheshi da zinariya." Cikin sauri sai saurayin ya mika mata tsuntsun.
"Gashi ranki ya dade na baki shi kyauta....tsaka nina da ke babu ciniki." Gimbiya Hussaina ta karbi kanarin cikin mamaki.
"Wai shin da gaske kake yi?"
"Tsakanina dake babu tsokana ko wasa ranki ya dade." Saurayin ya bata amsa.
"Na gode madalla da wannan kyauta da ka yi min ba zan taba mantawa da kai ba."
"Farin cikinki, farin cikina ne ranki ya dade."
Hussaina ta ji dadin abin da ya ce cikin zuciyarta.
"Ka ce kai mafaraucine ko?" Saurayin ya gyada kai.
"Yanzu yaushe za ka koma?" Saurayin ya sunkuyar da kai ya ce.
"Ni da asan samuna ne ma yau zan koma daji da daddare."
Kudi da Maciji...
Part (12)
Ga mamakin saurayin sai ya ga yar sarkin ta sunkuyar da kai cikin damuwa tana jujjuya kyakkyawan kanarin dake hannuta. A zuciyar saurayin ya ce.
"Kanarin ma har yafi dacewa da ita fiye dani, dubi yadda ta rikeshi sai suka yi kyau a tare tamkar taurari biyu karama da babba."
"Dole ne sai ka koma yau din?" Gimbiya Hussaina ta tambaye shi. Saurayin ya girgiza kai ya ce.
"Ba dole bane ranki ya dade, amma in da zai sami yadda nake so dai nafi son na yi tafiyata yau domin zaman gida shi ke mayar da mutum rago."
"Ni kuwa da asan samuna ne zan so mu sake haduwa anan bayan kwana biyu." Saurayin ya ji gabansa ya fadi ris! Tutuni ya rigaya ya sani cewa rayuwarsa na cikin hadari, domin yana tattare da masaniyar cewa kyakkyawar budurwar dake tsaye gabansa yar sarki ce.

"Ko kuwa baka son ka kara ganina ne?"
Hussaina ta ce dashi cikin rarraunar murya sa'ar da ta ga ya kasa magana. Cikin sauri sai saurayin ya girgiza kai ya ce.
"Duk duniya babu wanda ya isa ya ce baya kaunar ya sake ganinki ranki ya dade." Hussaina ta ji wani dadi ya lullube mata zuciya, dan haka sai ta dada matsowa kusa da shi ta ce. Cikin murmushi.
"Zan fi jin dadi a zuciyata idan ka kirani da sunana Hussaina maimakon ranki ya dade." Ta dan yi shiru tana kallonsa da dara-daran idanunta farare masu jirkita hankalin mazajen duniya.
"Gashi kuma har zamu rabu ban san sunan wanda ya yi min kyauta ba." Saurayin ya dago da kai a kunya ce bakinsa na rawa ya dubi kyakkyawar fuskar yar sarkin ya ce.
"Sunana AMADI DAN ZANGERU!"
***
ZANGERU ya dubi MAKWARO a cikin hasken farin watan, kana ya yi kaki ya tofar a cikin tarin ciyayin dake dab dasu cikin damuwa.
Na rasa abin da ya hana mai Masaba zuwa Zangeru ya ce da makwaro lokaci guda kuma ya sake duban yar siririyar hanyar da ta bi ta bayan gidansa har zuwa cikingari.
"Me yiyuwa ko sarkin dogaran ne ya hana shi tahowa ka fa san shi da shegen surutu."
Makwaro ya ce.
Mutanen biyu dake zaune cikin duhun daren suna jiran mai Masaba tun kafin shigowar almuru suke gurin, domin kowannensu tattare da masaniyar cewa yau ce ranar da Mai Masaba zai zo musu da karin bayanin karshe a game da gaggarumar satar da suke shirin yi.
Wannan mutum dake zaune kusa da Zangeru sunansa Makwaro. Dan gajerene mai fadi a dunkule yana da katon kai kamar murhu, hakanan idanunsa yan mici-micine kamar idanun maciji, bakinsa tsakakkene kamar gidan tsutsa. Yana da faffadan hanci tababbe wanda ya mamaye kusan rabin fuskarsa hakanan ya sa duk kusan yan matan garin suka tsane shi. Tun makwaro yana

saurayi bai taba yin budurwa ba, kuma har yanzun nan da yake dan kusan dan shekara arba'in da daya bashi da aure, sai tarin muguwar bakar zuciya wacce ta sa kusan kullum makwaro a cikin kunci yake da bacin rai, akwai sa'ar ma da shi kansa yake jin haushin kansa da kansa.
Tun sa'ar da uwar Makwaro ta haifeshi ta bar duniya, mahaifinsa shi ne sarkin maharban garin, har ya mutu bai taba kuskuren harbin duk naman dajin daya sa a gaba ba sai sau daya jal! Shima wannan hannunsa ne ke ciwo. Duk wani salon iya harbi kwari da baka na mahaifinsa, sai da Makwaro ya hardace shi har ma yafi mahaifinsa ko dan yatsa ka daga masa zai iya harba da kibiya babu kuskure, wasu ko suka ce wai ko kurciya ce ta zo wucewa ta sama idan yada gama yana iya harbin tsinin bakinta ba tare da ya kuskure ba, An ce kuma wai wani shakiyin kauye ya taba cewa da makwaro in har shi ya isa mai iya harbi, to ya bari sai kakansa ya hau saman bishiya saran ita ce, Makwaron ya sa kibiya ya harbi saman hancin tsohon amma kada jini ya zuba sosai. Haka kuwa aka yi Makwaro ya harbi tsinin hancin, to sai dai kuma abin yazo da ajali domin tsohon ko kwana bai yi ba ya ce ga garinku nan.
Wannan da kuma wasu dalilan na kwarewar Makwaro a fagen iya harbi su suka sa Zangeru da Mai masaba suka zabe shi a matsayin cikonsu na uku a shirin wannan gagarumar sata da suke shirin yi. Zangeru ya riga ya dade da sanin cewa Makwaro ma kwararren barawo ne, to sai dai kuma shima kamar su har yau satar bata tsinana masa komai ba dan haka sa'ar da Zangeru ya tunkare shi da batun satar sai Makwaro ya kada baki ya ce.
"Daman kullum fatana kenan, na yi gagarumar satar da duk labarinta zai watsu a duniya."
wannan shi ne halin Makwaro, har kullum ya fi son neman suna fiye da abin duniya.
Mutanen biyu suka ci gaba da zama cikin duhun daren, fuskarsu sai naso take da gumi kamar waina, kowannensu na sakar zuci.

"Ko jirana zaka yi anan na bi bayansa".
Zangeru ya ce da Makwaro. Makwaro ya mirgina
uban kansa mai kamar masaba ya ce.
"Ka ji kamar motsin tafiya ma nake ji ka ji ko..."
mutanen biyu suka yi fakare suna saurare kamar
zakaru. Tabbas sautin tafiya ne. Ba a dade ba
kuwa sai suka hango zabgegiyar surar Mai
Masaba a cikin dan hasken farin watan, yana tafe
cikin sauri, inda su Zangeru suke zaune kusa da
wata tsohuwar rumfa ce da ta gaji da tsayuwa ta
fadi.
Shekara da shekaru an rasa mai dogara mata ta
tashi.......
Kudi da Maciji... (13)
Lokacin da mai Masaba ya zo wucewa ta
kusa dasu bai gansu ba, domin shi duk a
tunaninsa a gida su Zangeru zasu yi jiransa.
Yana zuwa dab da gurin sai ya ji muryar
Zangeru ta ce.
"Ga mu anan, tun dazu kai muke jira." Mai
Masaba ya yi turus! Sannan ya juya gami da
kashe idanu a cikin dan hasken farin watan,
sannan ne to ya hangi mutanen biyu kamar
aljannu rakuye a bayan tsohuwar rumfar.
Mai masaba ya matsa kusa dasu kana ya saki
wani tattausan murmushi, sa'ar da ya hangi
katon kan Makwaro.
"Ashe kune anan". Mai masaba ya ce, sannan
ya zauna a kusa dasu.
"Ya ya ake ciki, bamu labari mu sha tun kafin
almuru muke nan make muna jiranka ni da
har na fara shawarar binka ma."
Mai masaba ya wangame baki kamar kada ya
yi wata doguwar hamma sannnan ya dube
su ya ce.
"Samun labarin babu wuya. Domin tun
la'asar mutumin namu sarkin dogarai yazo
shi da wasu fadawa daukar akwatin. Ka
sanshi da son banza, da man tun kafin ya zo
na sa matata Habi ta dama masa fura ta
zuba masa zuma a ciki. Ai yana fara shan
furar nan sai ya fara zuba kamar ruwan
sama, ni ko damar bugun cikin nasa ma ban

yi ba har sai da ya amayar min da komai."
Mai masaba ya dan yi shiru yana susar kugu. Dan tsawon lokaci sannan sai ya ci gaba da cewa.
"A cewar sarkin dogarai su shida ne za su raka akwatin, kuma jibi da daddare bayan isha za su tashi, to sai dai kuma akwai wani abu da ke tattare da tafiyar wanda mu ba mu yi tsammaninsa ba." mutanen biyu suka dubi mai masaba sa'ar da ya yi shiru.
"Kamar me kenan kake nufi?" Zangeru ya tambayeshi. Mai masaba ya yi atishawa ya ce.
"Akwai yara guda biyu matasa yayan sarki da su za a yi tafiyar." Mai masaba ya dubi Zangeru sa'ar da ya fadi batun. A karo na farko sai Makwaro ya girgiza katon kansa ya ce.
"Menene abin damuwa dan zasu tafi da wasu matasa? Ba sai na yi maganinsu ba. Ni abin da kawai ma yafi damuna shi ne idan mun kwace akwatin a ina zamu boyeta kafin kura ta lafa, kun san fa da zarar mun yi nasara duk hankulan sarakunan yankin nan zasu tashi musamman ma aminan sarki Sabitu, bincike na farautar mu zai tsananta don haka dole ne mu san inda zamu boye akwatin kafin kura ta lafa." jin haka sai Zangeru ya dubi mai masaba ya ce.
"Makwaro fa yazo da babbar magana me kake gani za a yi?" Mai masaba ya dube su ya ce.
"Ai wannan mai sauki ne, ni daman tuntuni na gama tunanin wannan matsalar har ma na gama maganinta a zuciyata."
"Menene to maganin matsalar!" Suka tambaya baki daya cikin doki. Mai masaba ya kaiwa kakkauran wuyansa duka da tafkeken tafin hannunsa sa'ar da wani kwaro ya fara safa da marwa akan dogon wuyansa.
"Ni abin da nake gani shi ne me zai hana idan mun kwace akwatin, mu koma da ita cikin katon kwarin nan dake kusa da

fadamar Danmasu wacce ke makwabtaka da gandun sarki sai mu haka rami mu binneta a gurin gindin wata bishiyar giginya."
Yana gama fadin haka sai Zangeru ya fashe da dariya ya ce.
"Ba ka da hankali mai masaba, in ba hauka ba me zai sa mu saci kayan sarki mu rasa inda zamu boye shi sai a kusa da gandunsa?"
Mai masaba ya dubi Zangeru shekeke ya ce.
"Abin da yasa nace mu binne akwatin anan shi ne, idan bincike ya tsananta babu wani mutum daga cikin baradan sarki da zai taba tsammanin za a boye akwatin a gurin. Na san da zarar mun kwace akwatin, duk hankula zasu koma ne kan garuruwan dake makwabtaka damu, wannan shi ne dabarata."
Zangeru ya dubi Makwaro. Makwaro ya dubi Zangeru sannan sai suka gyadawa juna kai. Mai masaba ya dubi mutanen biyu ya yi murmushi.
"Ina fatan kun fahimceni." Mutanen biyu suka gyada kai, sannan ne to Zangeru ya ce.
"Ka tambayi sarkin dogarai hanyar da za su bi?" Mai masaba ya gyada kai.
"Ta jikin duwatsun zungura za su bi, daga nan sai su yi yanke ta mararrabar kudu domin wai hanyar zata fi musu sauri."
Zangeru ya gyada kai sannan sai ya dubi makwaro ya ce.
"Makwaro sarkin maharba wacce irin shiga kake ganin za mu yi musu?" Makwaro ya mirgina uban kansa ya ce.
"Abi da zamu yi sai mu zagaye su, ku sai ku tare su ta gaba ni kuma na boye a bayan duwatsun.
Daga sun bullo sai ku fara yi musu ruwan kibiya, idan sun fara mayar da martini, sai na fito ta bayansu na fara habo su daya bayan daya har sai na kare su!" Zangeru ya dubi katon kan Makwaro ya ce "Yaya kuma zamu yi da yan kyawawan yaran nan yayan sarki?"
Mai masaba ya buda baki zai yi magana

kenan sai makwaro ya yi farat ya ce.
"Ba na ce daku zan yi maganinsu ba?"
Zangeru ya ji zuciyarsa ta harba, idan har akwai abin da ya ki jini shi ne kisan kyawawa. Yawun bakinsa ya kafe sa'ar da ya tuna da irin tsabagen kyawun yar sarki Gimbiya Hussaina.
"Me za ka yi musu?" Makwaro ya dubi Zangeru da fuskar katako ya ce.
"Kashe su zan yi dan babu ruwana da kyawunsu!"
***
Yau kwana biyu kenan daidai, tun bayan haduwar Amadi da Gimbiya Hussaina Haka nan ita ce ranar da ta yi daidai da alkawarin sake haduwarsu a bakin fadamar kamar yadda Hussaina ta bukata.
Kudi da Maciji... (14)
Lokacin da Hussaina ta isa bakin fadamar sai ta yi mamaki sannan ta tsunduma cikin damuwa domin ta dauka za ta zo ta tarar da Amadi a gurin zaune yana jiranta. Maimakon hakan sai ta iske tsuntsaye burjuk a bakin fadamar suna ta kai kawo abinsu suna wakoki cikin muryoyi iri daban-daban da masu dadi da masu ban haushi kai ka ce bikin yar sarkin tsuntsaye ake yi.
Gimbiya Hussaina ta yi tsaye bakin korama tana yan waige-waige, amma babu ko motsin Amadi. Cikin damuwa da tsananin fargaba me yiyuwa ma ba zata sake ganinsa ba sai Hussaina ta nufi dutsen nan da ta same shi wancan lokacin zaune akai ta zauna sannan ta zubawa tsuntsayen dake bakin koramar idanu bata ko kiftawa. Gashi dai a zahiri idan ka dubeta kamar tsuntsayen take kallo amma a badini ba su take kallo ba, babu abin da zuciyarta ke zayyana mata sai kyakkyawar surar dan saurayi Amadi.
Gimbiya Hussaina ta tuno da daren jiya, ta tuna da cewa ko da daidai da barcin sa'a guda bai zo idanunta ba. Tun sa'ar da suka rabu da kyakkyawan saurayin ta koma gida

sai ta kasa zaune ta kasa tsaye.
"Me ke damunki ne?" Hassan din ta ya tambayeta sa'ar da suke zaune tare da shi bayan almuru. Gimbiya Hussaina ta dubi dan uwanta Hassan sai ta rasa me zata ce dashi, domin ita dai ta san har suka rabu da saurayi babu wata bayyananniyar magana a game da soyayya da ta shiga tsakaninta da shi, to amma kuma zuciyarta ta rigaya ta san ta kamu da ciwon son wannan kyakkyawan saurayi. A da can wani lokaci idan Hussaina tana karanta labaran soyayya a cikin litattafan larabawa ta kan ga wautar mata da suke nacewa akan son da namiji, domin a ganinta wauta ce kawai, yaushe ne ma za a ce kamar ita yar sarki ta kamu da ciwon son wani mutum talaka wanda shi bai ma damu da ita ba. Amma a yanzu da yake Hussaina ta tsinci kanta a cikin irin wannan yanayi sai ta fahimci ashe dai matan nan da ta sha karanta labaransu a cikin littattafan larabawa basu da laifi, ashe daman haka so yake kamar sartse!
Kwanaki biyun da Hussaina ke jira su zo sune mafiya tsayi da ta taba gani a rayuwarta, domin a washe garin ranar da suka hadu da Amadi sau daya tak ta sami damar cin abinci. Koda ta sa abincin ma a bakinta sai taji babu dadi kamar tana cin danko, haka nan duk sa'ar da ta tuna da Amadi sai ta ji zuciyarta na harbawa. Gimbiya Hussaina ta ci gaba da Allah-Allah gari ya sake wayewa ko ta sake dora idanunta akan Amadi. Rana ta fara haske amma Hussaina gani take yi kamar ma yamma ba za ta yi ba a ranar ballantana, kuma har gari ya waye ta sake ganin Amadi. Da aka jima Hussaina ta fahimci kamar ranar ba ta yi mata sauri, sai kawai ta koma daki ta kwanta da zummar wai ba zata farka ba sai magariba.
Lokacin da ta farka sai ta ji a lokacin ne ma ake kiran sallar Azahar.
Abubuwan suka taru suka dagule mata.

Zuciyarta ta fara bata shawarar mai zai hana idan ba za ta iya daurewa ba ta dauki kuyanginta su raka ta har gidan su Amadi mana. Ai kuma abin kunya ne ace yar sarki tabi talaka har gida. Wata zuciyar tace da ita. Dan haka a yanzu da Hussaina ke zaune akan dutsen tana jiran isowar Amadi cikin rashin tabbaci, sai ta yanke hukuncin cewa in har aka jima bai zo ba, ko shakka babu gida zata bishi.
Gimbiya Hussaina ta dan zame kadan daga kan dutsen da take zaune sannan ta zura kyawawan kafafunta cikin fadamar ta fara wasa da ruwa.
A daidai wannan lokacin ne ta ji motsi a bayanta.
"Ki yi hakuri ranki ya dade Allah ya huci zuciyarki na ajiyeki zaman jira." wata sassanyar murya ta ce daga bayanta.
Hussaina ta ji wani irin dadi ya mamayi zuciyarta, cikin farin ciki ta juyo gare shi da tattausan murmushi akan jajayen lebbanta.
"Sannu da zuwa Ammadi...ina fatan dai lafiya?" Amadi ya dubeta da murmushi ya gyada kai.
"Lafiya lau ranki ya dade wallahi mahaifina ne ya tsayar dani." Hussaina ta lumshe idanu cikin farin ciki.
"Ni da na dauka ma ba za ka zo ba." Amadi ya girgiza kai cikin gaggawa.
"Haba ranki ya dade, ni na isa ki yi kirana na ki zuwa...saboda tunanin alkawarin nan naki ko cikakken barci bana yi."
"Saboda me?" Hussaina ta tambayeshi.
Amadi ya sunkuyar da kai kusan na tsawon lokaci bai amsa ba, sannan daga karshe sai ya dago kai ya ce.
"Saboda da na rufe idanuna sai na yi ta ganin surarki ranki ya dade....ga shi kuma tunanin kirkinki da karimcinki ya kasa barin zuciyata." Hussaina ta ji dadi ya sake mamayar zuciyarta a karo na biyu. Ta dago kanta ta dubeshi ido-da-ido ta ce.

"Amadi wannan shi ne kawai abin da ya hanaka barci ko kuwa akwai wani abin daban."
Amadi ya dubeta cikin rashin fahimta ya ce.
"Ban fahimce ki ba ranki ya dade." Hussaina ta sunkuyar da kai a wannan karon kana sai ta ce cikin wata rarraunar murya.
"Ni kuwa tunaninka... Da kaunarka ce suka hanani barci."
"Zuciyar Amadi ta harba tsakawa hakarkarinsa kamar zata huda ta fito. Bai taba tsammanin za ta fito fili ta bayyana kaunar tata a gareshi ba.
"Ranki ya..." Amadi ya yi shiru bai karasa ba sa'ar da ya ga Hussaina ta daga masa hannu.
Kudi da Maciji...
Part (15)
"Hussaina sunana, ina fatan ranki ya dade din nan zata fita daga bakinka." Ta yi masa murmushi sannan sai ta matso kusa da shi ta ce.
"fada min da bakinka Amadi kana sona."
Amadi ya ji zuciyarsa ta yankwane a guri guda ko shakka ba ya yi ya san yana kaunarta, domin shima abinda ya hana shi barci kenan a darare biyun da suka wuce, to amma shi yasan wannan soyayya dake kokarin faruwa a tsakaninsu tamkar soyayyar mafarkice domin ina shi ina yar sarki!
"Ranki ya....Hussaina...tun sa'ar da na fara dora idanuna a kanki na ji ina kaunarki to amma ni na rigaya na sani bazan taba samunki ba domin babu hadin dan talaka da dan sarki."
"Kada kace haka Amadi, domin kai baka san gaibu ba...in Allah ya so kaine mijina Amadi."
Amadi ya sunkuyar da kai. A zuciyarsa ya ce. Kai lamarin duniya na da ban mamaki ka ji kai yarinya saboda shaukin soyayya tana sambatun almara.
"Daman abin da ya sa na ce da kai ina son mu sake haduwa anan domin mu yi sallma ne, ka san jibi zamu bar garin nan ni da dan uwana Hassan."
Amadi ya dubeta cikin mamaki.
"Wane gari zaku koma?"

"Wajen babban aminin mahaifin mu za a mayar da mu sarki Lurwanu, na san me yiyuwa kasan garin tun da kai mafaraucine." Amadi ya gyada kai.
"Kwarai kuwa na san garin, domin wazirin sarkin Lurwanu yasha fansar fatun damisa a gurina." Gimbiya Hussaina ta yi ajiyar zuciya da jin cewa ya san garin.
"Idan kana ganin ba takurawa Zan so ka bini garin, amma ka bari har sai mun sauka a garin da kwana biyu, idan ka je zan tare ka a bayan gari. Ko ya ya ka gani?" Amadi ya gyada kai a tsorace ya ce.
"Duk abin da kika ce haka za a yi....Hussaina!" Hussaina ta dube shi cikin tsananin farin ciki ta ce.
"Na gade Amadina, duk duniya bani da na biyunka cikin ruhina." Amadi ya yi ajiyar zuciya gami da duban tsuntsayen dake jajjere a bakin koramar.
"Yanzu yaushe za ku tafi."
"Jibi war haka muna shirin tafiya garin kamar yadda muka yi alkawari."
Gimbiya Hussaina ta cire wani kyakkyawan zoben azurfa dake dan yatsunta ta mikawa Amadi.
"Ga wannan ka ke tunawa dani kafin mu sake haduwa, ni kuwa zan tafi da kanarin da ka bani cikin keji, ya isheni debe kewa tunda dai kyautar ka ce."
Matasan biyu suka kurawa juna idanu suna murmushi, domin basu sun rabuwa.
Da sun lura da kyau, za su hangi wata farar babelar daga can cikin tsuntsayen bakin fadamar tana kallonsu cikin tsananin mamaki da kaduwa!
***
"Lah ka ga dogayen duwatsun nan da baba ya sha bamu labari." Hussaina ta ce da dan uwanta Hassan cikin doki, lokaci guda kuma ta mika hannunta daga kan dokin ta taba dutsen da kyakkyawan yatsanta. Hassan ya dubi dutsen a yatsine sannan ya dubi yar uwarsa Hussaina ya ce.
"Kin ga ni kuwa babu abin da na tsana a rayuwata irin dogayen duwatsu."

"Me yasa?" Hussaina ta tambaye shi gami da murmushi, domin ta riga ta san tafi dan uwan tagwaitakar jarumta.
"Kawai dai ni son ganin dogayen duwatsu ne ba nayi, wata sa'ar sai in ga kamar mutuwa ce ke kokarin zuwa ta zare ni musamman ma a irin wannan lokaci na duhu." Hussaina ta bushe da dariya.
"Kai dai wallahi matsoraci ne, in ba haka ba ka taba ganin an gujewa mutuwa? Ai duk inda kwananka ya kare ko a akan duwatsu, ko a cikin fadar babanmu sarki, ko a cikin duhu ko a hasken ran sai mutuwa ta riskeka domin idan ta zo babu tsimi babu dabara." Hassan ya dubi yar uwarsa da murmushi a cikin duhun daren.
"Wannan gaskiya ne, ya yar uwata Hussaina." Sarkin dogarai dake daf daf da su ya yi murmushi a cikin duhun daren sa'ar da ya ji hirar da ke gudana tsakaninsu. Sannan kamar yadda ya saba fadi kullum cikin zuciyarsa, yanzun ma sai ya ce ina ma ace yayansa ne. Sarkin dogaren ya juya baya ya dubi yan rakiyar tasu mutum shida ko wannensu cikin shigar yaki, dauke da kibbau masu dafi, suna tafe sun sa kakkarfan dokin da aka dorawa akwatin dukiyar a tsakiya, wata sa'ar ko motsin ganye suka ji sai sun juya da shirin kai sara. Kamar macizai.
Duk da wannan shiri da barazana da suke yi basu taba tsammanin wani abu makamancin fashi zai faru a kansu ba, domin sun yi imani da cewa duk wani barawo dake hanyar ya san da irin jarumtarsa ta baraden sarki, a tunaninsa babu mai iya tunkararsa da wata barazana.
"Mutanen duniya basu da tabbas, suna iya ba ku mamaki." Sarkin dogarai Hambara ya ce da su sa'ar da za su baro gida. Wannna shi ya sa baraden yan rakiya daukar takubba sabanin kwari da bakan da suka dauka tun farko.
A can gefe guda a bayan duwatsun cikin duhu Makwaro ne zaune ya dana kibiyarsa ta farko wacce da ita ce yake fatan mika sarkin dogarai lahira, tare da sauran jama'arsa. A can kuma karshen duwatsun sarkin barayi Zangeru ne shi

da abokinsa sarkin makera da barayi Mai masaba, sun yi kwanto suna jiran karasuwar tawagar ayarin. Tun farkon shigowar almuru suke nan makale, har sun fara kosawa, saboda tsabar rikon kibiya a dane har hannun Zangeru ya fara gumi.
Suna nan makale, lokaci guda kuma suna makyarkyatar sanyin asuba da ya fara hurowa, wata sa'ar jikinsu har buguwa yake da na juna kamar zakarun da ruwa ya jika......
Kudi da Maciji... (16)
A daidai wannan lokacin ne to suka jiyo motsin ayarin tawagar sun doso inda suke boye.
Mutanen biyu sarakan barayi suka dubi juna, lokaci guda kuma suka hangi inda Makwaro yake make.
Daga inda suke zaune suna iya hango rungumemen kan Makwaro wanda ke zaune ya yi dani, baya ko motsi kamar gunki.
"Allah ya sa dai kada lalataccen can ya harbi yaran nan biyu... "Zangeru ya ce, ba tare da ya dubi Mai masaba ba. Domin tuni har sun fara jiyo hayaniyar mutanen suna hira.
"Ai kuwa in ba wata sa'a ba da nisan kwana sai ya kashe su, ka ga dai sana'armu daya da shi amma wallahi ni kaina tsoron rashin imaninsa nake yi."
Zangeru ya ji wani zazzafan gumi ya fara yi masa sartu a doron baya. Har ga Allah ba shi son abin da zai sa a kashe kyawawan yayan sarkinnan domin shi dukiyar ce kawai agabansa ba kisan kai ba.
"To sai fa gare mu ga sunan sun matso." Mai masaba ya ce da Zangeru sannan cikin zafin nama na ban mamaki sai ya gyara danin kibiyar dake jikin bakansa, sannan ya cilla harbi cikin ayarin ta tsakanin duwatsun. Ba a dade ba suka ji an kwalla kara mai tsanani, sannan sai sautin fadowar wani mai sauti irin na buhun sumunti.
"Na sami daya kafiri!" Mai masaba ya ce cikin karaji Zangeru jiki na rawa ya shafi gefen

tsafaffen bantensa inda ya kulle dutsen nan da balbela ta bashi, ya tabbata yana nan, sannan sai shima ya cilla harbi cikin ayarin. Nan da nan hayaniya ta barke da hargowa, da ife-ife cikin razana da kaduwa. Daga cikin duhun Zangeru ya hangi Makwaro ya fara cilla harbi cikinsu, har sau uku, duk harbin da yayi sai ya jefa mutum daya kasa.
Ba a dade ba sai wajen ya yi tsit. Baka jin komai sai gurnani da motsin dawakai. Mai masaba ya dubi Zangeru jikinsa na rawa yana haki ya ce.
"Mun ci nasara....lalat accen duk ya kwantar da su." Zangeru bai ko dubeshi ba, jikinsa sai kyarma yake yi. Abin da ke damun zuciyarsa shi ne." kyawawan yaran yayan sarki, ko shakka ba ya yi makwaro duk ya harbesu. Ya kuwa tabbatar kibiyar Makwaro tsafaffiya ce ba ta sukar mutum ya rayu. Ga mamakin Zangeru sai ya ji akaro na farko ya tsani kansa ya kuma tsani Makwaro, don me....saboda me a wane dalili zai kashe wannan kyakkyawar budurwa ita da dan uwanta bayan shi kuma nasa dan Amadi yana can gida lafiya kalau babu ko kwarzane a jikinsa.
"Wayyo Allah na shiga uku na lalace wayyo Hassan!" Ihun Hussaina ya ratsa cikin dajin, amsa kuwwar ta watsu cikin duwatsu. Sarakan barayin biyu suka dubi juna, sannan lokaci guda suka dubi inda Makwaro yake. Kotsam sai suka ga ya mike tsaye, ya zaro kibiya daga cikin kwari ya danata sannan sai ya yi awon cikin duhun inda suka ji ihun tun farko. Zangeru ya ji zuciyarsa ta harba domin ya san abin da Makwaro ke nufin yi. Cikin zafin nama na mamaki sai Zangeru ya dana tasa kibiyar ya saita wuyan Makwaro ya harba. Kamar wasa sai kibiyar ta sami inda aka yi nufinta. Makwaro ya kwalla ihu sannan sai ya fadi a gurin. Mai masaba ya dubi Zangeru cikin kaduwa ya ce.
"Haba Zangeru! Kanka daya kuwa? Me yasa

zaka harbeshi?" Zangeru ya harari Mai masaba a cikin duhun ya ce a fusace.
"Me yasa zai kasheta, bayan kuma da sauran kwananta a duniya, ko ya dauka shi kadai yake da tsafin harbi, yau ko kunama ne shi na kawo karshen karyar banza!" Mai masaba cikin kaduwa ya mike tsaye a fusace.
"Ba zata yiyu ba Zangeru., dole ne itama ta mutu, idan kai ba zaka iya taba ta ba, bari ni in tafi na karasata."
Yana gama fadin haka sai ya fara gangarawa kasan dutsen ya nufi inda suka jiyo ihun budurwar.
A daidai wannan kokacin ne to Zangeru ya ji kamar wani abu na sukansa a kugu. Cikin sauri ya kai hannu gurin sai ya ji ya taba tsinken kibiya. Jikinsa na rawa ya zare daga kugunsa ya dagata sama a cikin duhun daren. Ko shakka ba ya yi daya daga cikin kibiyoyin da baraden sarki suka sami damar harbowa ce ta huda bantensa ta kuma dan soke shi kadan a kugu. Babu mamaki tashin hankaline ya hana shi jin sukar kibiyar tun farko. Zangeru ya yi kamar ya jefar da kibiyar da ya zare daga kugunsa, can kuma sai ya fasa, lokaci guda kuma ya ji wani zazzafan gumi ya fara wanke masa fuska. Ya sha jin labarin cewa duk kibiyoyin dake kwarin baraden sarki a shurbune suke da masifaffen dafi wanda duk wanda ya soka ba zai rayu ba.
Daga inda zangeru yake tsaye yana iya hangen faffadan bayan Mai Masaba wanda ke gangarawa a hankali ta tsakanin duwatsu.
"Kyakkyawar budurwar yarinya ce karama, bai kamata ta mutu tun yanzu ba, ni kuwa tawa ta kare, kamata ya yi mu wuce lahira ni da babban abokina." Zangeru na gama fadin haka sai ya shafi kugunsa inda kibiyar ta same shi. Bai yi mamakin jin gurin tuni har ya fara kumbura ba. Ya ji wani zafi ya soki kugun kamar ana hura masa wuta. Yanzu

kam ya tabbata dafi ne a jikin kibiyar.
Zangeru ya jinjina kibiyar a hannunsa, sannan sai ya dana ta, ya daga kwarin sama ya saita faffadan bayan babban abokinsa Mai masaba, sannan sannu a hankali ba tare da wata nadama ba domin ya san ceton rai yake yi sai ya saki kibiyar CUL!
By nazir adam salih
Kudi da Maciji... (17)
***
Lokacin da Zangeru ya dawo bakin katuwar koramar ta Danmasu, tuni har gari ya gama wayewa. Yayi sa'a bai hadu da kowa ba sai wata tsohuwa mai sammakon tsiya dake bayan gari a musissika dake daf da koramar tana shikar gero.
"Sannu da zuwa bawan Allah." Tsohuwar ta ce da Zangeru sa'ar da ta ganshi tafe bisa katon dokin dauke da akwatin karfen yana tafe yana layi kamar zai fado daga kan dokin, sakamakon dafin kibiyar da ke daukarsa. Zangeru bai ko dubi tsohuwar ba, ya wuce kai tsaye zuwa can cikin koramar jikinsa na ta rawar dari sakamakon mummunan zazzabin dake addabarsa, lokaci guda kuma zuciyarsa na ta tunanin halin da Hussaina take ciki.
Lokacin da Zangeru ya tabbatar ya harbe babban abokin satarsa Mai masaba, ya gangaro daga kan dutsen yana layi, ya shigo har inda tawagar baraden sarkin suke duk a kwankwance, kuma a marmace. Bayan da ya tabbatar babu mai wani sauran numfashi, sai ya fara laluben inda Hussaina take, ya dade yana lalube kafin ya gano ta karkashin wani lankwasasshen dutse mai siffar bil'adama tana kwance a sume. Zangeru ya jujjuyata na dan lokaci ya tabbata suma ta yi ba mutuwa ta yi ba sannan sai ya dafa ta ya yi abin da rabonsa da yi tun yana karami, addu'a.
"Allah kareki kyakkyawa, Allah sa fatake su tsinceki." Yana gama fadin haka sai ya nufi inda nan, dokin akwatin dukiyar yake, ya yunkura ya haye bisa dokin, ya juyo ya kalli gawarwakin kallon karshe sannan sai ya karkata linzamin dokin ya bi ta kan gawar babban abokinsa

marigayi Mai masaba ya koma da baya.
Dan haka a yanzu da Zangeru ya zo bakin korama sai ya hangi wata doguwar bishiyar giginya dake gangare. Ba a nan ya so ya tsaya ba, to amma da yake jikinsa ya gama yin rauni sai ya sauka a gurin. Bai yi mamakin jin kafafunsa sun kasa daukar nauyinsa ba. A haka sai ya fadi a gurin zaman yan bori, bai damu ba domin tuni ya shirya abin da zai yi cikin zuciyarsa. Jikinsa na rawa ya lalubi inda ya kulle farin DUTSEN NAN a cikin bantensa, ya kunto dutsen, sannan sai ya sa dutsem tsakanin tafin hannunsa biyu ya murza.
"Gani Zangeru, me kake so masoyina." Farar balbelar ta ce sa'ar da ta bayyana a gabansa. Zangeru ya dubi balbelar yana haki bakinsa na rawa ya ce.
Dan lokacin da ya rage min a duniya kadan ne, shi yasa na neme ki domin ki yi min taimakon karshe kuma mu yi sallama kafin na mutu."
"Me kake so?" Zangeru ya dubeta ya ce kai tsaye.
"So nake ki sa yan uwanki aljanu su tona rami..
PAGE DIN NAN YA YI (damage) zamu tsallake...
Shima jiya Allah ya yi masa rasuwa. Ina son ki layar nan da kyau ko da Allah bai kaddara aurena da ke ba, ina son idan kin haifi da ko ya ke ma ki basu layar domin na fada miki maganin tsautsayi ce sosai, don da ita mahaifina ya yi ta amfani har iya rayuwarsa." Hussaina ta dubi Amadi a razane da jin abin da ya ce lokaci guda kuma ta dubi layar da yake mika mata ta ce.
"Me ya sa kake irin wadannan maganganun? Wa ya ce ma ba za ka aureni ba?" Amadi ya dubeta cikin damuwa ya ce.
"Ke kin san abin ne da wuya Hussaina..." Ta kate shi.
"Amadi, shi yasa na ce ka mayar dani gida domin idan mun je zan ce da mahaifina kaine ka ceci rayuwata a hannun barayin....na san tabbas idan ya ji haka na nuna ina kaunarka babu abin da zai hana ya aura min kai."
Tabbas maganar da ta fada ta yiwa Amadi

ma'ana, to amma duk da haka sai ya dada mika mata layar ya ce.
"To gashi dai ki rike layar a gurinki, idan Allah ya sa kin aureni din idan mun sami da ba sai mu sa masa ba."
"Me yasa to kai ba zaka rike layar a gurinka ba?"
"Saboda maganin tsautsayi ce na fi son na ganta a gurinki. Bari na sa miki ita." Kafin ta rufe baki Amadi ya rataya mata layar a wuya, sannan sai ya dubeta ya ce.
"Zo mu tafi." Hussaina ta juya hawaye na zuba akan fuskarta ta yiwa gawar dan uwanta ganin karshe sannan sai ta juya gami da dafa layar dake makale a wuyanta ta bishi a baya.
Koda suka fara tafiya sai suka ji haniniyar doki a bayansu. Hussaina ce ta fara juyawa cikin mamaki. Dokin ya yi haniniya sa'ar da ya fito daga cikin duwatsun sannan sai ya nufo inda suke.
"Lah! Allah sarki ashe kaima Allah bai kari kwananka ba." Amadi ya juyo ya dubeta ya ce.
"Wanene?" Hussaina ta nuna masa shi da hannu ta ce.
"Dokina ne da nazo a kansa." Amadi ya ji wani dadi ya lullubeshi a karo na faro, domin babu abin da ya tsana irin ya ga Hussaina ta taka a kasa har zuwa garinsu mai nisan tsiya daga gurin.
"Na gode Allah da ya kawo miki abin hawa."
"Kai fa ba zaka hau ba." Amadi ya girgiza kai ya ce.
"Kada ki damu dani. Ke dai dafe layar nan dake wuyanki kada ki jefar da ita idan kin zo hawa dokin...me yiyuwa ki na cika mita akan layar nan ni kuma abin da ya sa nake ta magana a kanta saboda na san maganin tsautsayi ce."
KARSHEN BOOK1
Kudi da Maciji... (18)
>>>> Book (2) <<<<
Ga doki har doki, amma kofaton na sakaina. yar budurwar tace cikin zuciyarta a sanyaye sa'ar data dubi kanta a jikin dogon mudubin dake fuskantarta. Ba wani abune yasa ta fadi hakan ba sai hadin bautar ban haushin data gani a jikin

madubin. Gashi dai kyakkyawace doguwa mai tsukakkiyar mara fatar jikinta a mulmule tana sheki kamar kwalba a rana, hakanan dan iskan can da a kullum sai ya gallabeta a makaranta yasha cewa da ita.
"Kai!! Bebe wallahi ina son (Skin) din nan taki, gata dai ita ba fara ba, ba baka ba kuma ba jaba... (See you eyes) kyawawa juyayyu masu firgita lakcarori yayin daukan darasi, ga kuma fatan bakin ki (Looks very soft) tattausa shi yasa kullum nake kaunarki ke wallahi da ni malamin jami'a ne da har ki gama bake ba faduwa".
To amma duk da irin wannan kyawun nata sa'ar da ta dubi madubin sai taji ranta ya gama baci, badan komai ba kuwa sai dan yaroki-yarokin tsummokaran dake jikinta bana fita kunya a farfajiyar makaranta bane. Gata dai a tamfar ba wata mai tsada bace kamar buhun busasshen zogale, ta kokkode ta jeme kamar labulen laburari, hakanan dan siririn kallabin dake dafe akan kyakkyawan goshinta shima duk ya ji jiki yayi shara-shara kamar buhun algarara, ga kuma uwa uba abin dake dada bata mata rai a kullum wato bangwaleliyar LAYAR dake makale kullum a siririn wuyanta. Wannan laya tana matukar bata mata rai, ta tsani layar nan kamar yadda ta tsani dan iskan saurayincan na makarantarsu mai takurawa rayuwarta a kullum.
Yar budurwa ta sake kallom kanta a jikin madubi cikin takaici sannan sai ta shafi tsohuwar layar dake wuyanta wacce a cewear masifaffiyar marikiyarta wai layar ta dade a duniya kuma waita gado ce, tun daga can wajen kakanninta na farko ake ta gadonta har zuwa kanta. To koma dai ta mecece ita kam wannan budurwa ta tsani wannan laya, gashi dai ita ba wata suturar kirkice da ita ba, kullum taje makaranta a rarrabe take, bata iya shiga cikin kawayenta, badan komai ba sai dan ganin su kullum tsaf suke cikin sutura mai tsafta, amma ita kullum cikin tsumma, ga kuma wata layar masifa an makalamata a wuya.... To yanzu in ba son a muzantani ma wane yaro ne a wannan zamani za'ce wai dole

sai yasa laya. Hawaye ya fara surtu a kyawawan kumatunta yarinyara sa'ar data fara kokarin tura layar cikin rigarta.
"kukan me kuma kike yi A'ISHA?" wata fikakkiyar murya tace da ita daga baya. Aysha ta juya firgigit tadubi mai rikonta jikinta na rawa.
"Ma......ma ba komai"
"Ba komai kamar yaya? Amma kuma ba komai din kike kuka, ke dai wallahi Aysha kin shiga uku da gulma, shegiya masifaffiya uwar jaye-jayen magana wato yanzu tsakanina da ke ma abin har ya kai ga sharri ko? Yanzu idan wasu dangin namu suka shigo gidannan ai sai suce cutar maraya nake to Allah ya gani dai tsinanniya tunda iyayenki suka mace na daukeki ina faman wahala dake ashe bakar jaraba na dauka to kyaci kanki ba dai ki cinye niba zaki tashi ki tafi makarantar ko kuwa sai na karaso naci ubanki a nan in yaso kiyi kukan da dalili?".
Aysha ta mike a tsorace sannan ta dauki jakarta dake kan kujera cikin sauri ta fice daga dakin tanagoge idanu.
"saura kuma ki dawo na ga kin jefar da wannan laya wallahi na lahira sai ya fiki jin dadi yar iska" matar tace da ita tana bambami.
Aysha bata amsa ba sai ta fice tana kuka.
Karfe tara da kwata ta isa jami'ar, tuni tasan an fara daukar darasi, kuma tana tattare da masaniyar cewa muddin dalibi ya kara mintuna goma sha biyar to bashi ba shiga dakin darasin musamman ma idan Dafta Bashir ne ke koyarwa.
Tunanin hakan da kuma gudun kada taje shiga dakin karatun Dafta bashir ya muzantata a gaban dalibai, shi yasa Aysha ta karkata tabi ta cikin inda ake fakin da motocin daliban, domin nan ne kawai zata bi ta iya zuwa dakin kwanan dalibai mata dake jami'ar. Ko banza dai, Aysha tace cikin zuciyarta. Idan na je dakin kwanan daliban na dan wanke fuskata na gyara kwalliyata, kafin Dafta bashir ya fice daga ajin in yaso na halarci darasi na gaba.
A haka Aysha ta kutsa ta tsakanin tarin motocin burjuk kamar fari dake farfajiyar makarantar,

wanda mafi yawa daga cikin motocin duk na dalibai ne. A dai-dai lokacin da take kokarin wucewa ta kusa da wata marsandi ne to taji an rike jakar dake rataye a kafadarta ta baya. Aysha ta juya a fusace.
"Sannu da zuwa Aysha kema a makare yau kika zo?"
Aysha ta dubi mai magana cikin takaici tace a fusace.
"Dan Allah me yasa ne kullum kake son takurawa rayuwata!!"
"Ki gafarce ni Aysha wallahi so nake kawai mu gaisa, dan nasan idan muka shiga dakin karatu ba saurararata zakiyi ba".
"Kuma dan kana so mu gaisa sai ka rikemin jaka? Kai baka jin kunyar mutanen dake kallon ka, duba fa can, da nan ko'ina duk dalibai ne amma sai ka....."
"Aysha, kar ki zama kamar wata yar sakandare mana (Remember) fa yanzu a jami'a muke ba ruwan kowa dan haka idan ina soma (I can kiss you, I don't care)".
Kudi da Maciji... (19)
"Allah ya yi min tsari da kai!" Aisha ta ce a tsorace sannan ta fara ja da baya za ta wuce shi.
"Aisha! Saurayin ya kira sunanta a tausace. Ta sake juyowa a hankali kyakkyawar fuskarta a murtuke ta ce dashi cikin shisshika.
"Dan Allah dan Annabi ni ka kyaleni na huta, ka takurawa rayuwata, tun da na zo makarantar nan kake ta damuna da maganganu marasa ma'ana na rashin kunya, to ni na gaji, ka je ka nemi daidai da kai ni ba yar kowa bace dubeni fa?"
Ta daga hannu ta nuna masa tsummakaran kayan dake jikinta. Menene abin sha'awa a jikina, tsummokaran ko me?"
Saurayin ya zura mata idanu na tsawon lokaci yana kallon bangwaleliyar layar dake wuyanta, baya ko kiftawa tamkar malamin kimiyya mai nazarin kwayoyin halittun cikin

ruwa.
"Aisha, direshi kawai suka fiki ba kyau ba, amma nitun da nake ban taba ganin wacce nake kauna kamar ki ba, amma ke kin tsaneni, kullum ina lura da ke da na yi miki magana sai in ga kin hada rai kamar kin ga mutuwarki, sai kuma ki yi ta wulakantani."
Gaban Aisha ya fadi sa'ar da ta ji ance ta yi wulakanci.
"A'a...ka yi hakuri ni ban iya wulakanci ba...ni irin maganganunka ne bana so."
"To daga yau ban kara yi miki su, amma kauna ban iya dainawa Aisha kin shiga rayuwata har abada!"
Aisha ta sunkuyar da kai tan wasa da yan yatsunta, sannan sai ta dago kai matasan biyu suka dubi juna na dan lokaci. Saurayin ya sake kurawa layar dake makale a wuyanta idanu zuciyarsa cike da mamakin dalilin da ya sa wannan kyakkywar budurwa yar jami'a guda take yawo kullum da laya a wuya. Tun shekarar karatunsa ta farko a jami'ar yake ganinta da bangwaleliyar layar, da yawa daga cikin abokansa sun sha cewa dashi.
"Kai bebe din nan karshe ce duk fakalti din nan babu mai kyanta, amma rashin diresin da katuwar layar nan da ke wuyanta shi ya bata lamarin bayaninta."
Aisha ta yi sauri ta rufe layar da tafin hannunta sa'ar da ta lura da irin kallon da saurayin ke yi mata. Sannan sai ta juya tana cewa da shi.
"Sai an jima ko?" Saurayin ya yi murmushi cikin jin dadi domin tun da yake bata taba cewa da shi sai an jima ba.
"Aisha...a dawo lifiya. Idan an tashi kuma, zan so ki bani labarin wannan layar da ke wuyanki."
Fuskar Aisha ta sauya launi sa'ar da ta ji abin da ya ce.
"Babu ruwanka da layata." Aisha ta ce da shi, ba tare da ta tsaya ba. Tana gama fadin haka

sai ta dada sauri ta nufi dakin kwanan dalibai wanda dole ne sai ta bi ta tsakanin wani dan karamin daji-daji kafin ta kai dakunan.
Lokacin da Aisha ta biyo ta yar siririyar hanyar kusan ita kadai take tafiya domin duk kusan dalibai suna dakunan karatu suna daukar darasinsu na ranar.
A daidai lokacin da ta kawo kusa da wasu dogayen bishiyoyin turarene to ta ji an yi kiran sunanta a baya.
"Aisha!"
Cikin sauri Aisha ta juyo a tsorace domin muryar ba ta yi kama da ta mace ba, haka nan kuma ko shakka babu muryar bata yi kama da ta namiji ba. Sautin muryar ya fi kama da sautin muryar da aka yi amonta ta cikin bututun roba.
Aisha ta dafa kirji sa'ar da ta juyo tana waige-waige cikin fargaba domin bata ga kowa a bayanta ba sai wani famfo dake zubar da ruwa shi kadai a cikin tarin ciyayin dake karkashin bishiyoyin turaren gami da wata kyakkyawar balbela fara mai dogon wuya da tsinin baki, tana karkada fuffukenta cikin nishadi.
Aisha ta yi sauri ta gyara jakar dake kokarin subucewa daga kan kafadarta domin duk ilahirin jikinta rawa yake yi kamar mazari, sannan lokaci guda kuma ta fara waige-waige a rude.
"Shin ko ba sunana naji an yi kira bane?" Aisha tace cikin zuciyarta. Daga inda take tsaye tana iya hangen dalibai mata a can nesa da ita a kofar (hostel) din, hakanan kuma tana iya jiyo hayaniyar dalibai sama-sama acan cikin makarantar inda dakunan darussa suke.
"Lallai kam me yiyuwa kunnena ne yake fada min karya." Aisha ta sake cewa zuciyarta. Dan haka sai ta sake juyawa gami da yiwa kanta murmushi.
"Aisha yar yarinya ke dai kin cika tsoron

tsiya wallahi." Ta ce da kanta.
Tana juyawa gaba ta fara tafiya sai ta ji an sake cewa a bayanta.
"Aisha dake fa nake." Aisha ta yi mutuwar tsaye domin ko shakka bata yi ta san sunanta ne aka kirawo a wannan karon.
"Wa...nene!" Aisha ta juyo tana fadi a razane domin har yanzu ba ta ga mai kiran ba sai farar balbelar nan dake kan famfon nan mai tsiyayar da ruwa tana dubanta.
"Ni ce Aisha, kada kuma ki ji tsoro na ni mai kaunarki ce." Farar balbelar ce ke magana da Aisha ko shakka babu.
Aisha ta yi tsalle gefe guda a razane ta dubi balbelar idanunta kamar za su fado a kasa saboda tsabar kadawa. Balbela da magana, na shiga uku!! Aisha ta ce cikin zuciyarta.
Hannayen Aisha suka dauki rawa kar! Kar!! Kar!! Kar!! Jakar dake kafadarta ta kwace ta fadi akan tarin ciyayin. Nan da nan iska ta fara fatali da yan takardu da kuma litattafan Aisha a cikin ciyayin.
Dauki jakarki Aishata ba cutarki zan yi ba, tsakanina da duk danginku sai dai kauna.
Kudi da Maciji...
Part (20)
Na san tuni kin fara tunanin ko ni aljana ce, to tabbas haka ne ni aljanace kuma na dade ina tare da danginku yau kusan shekaru dari da ashirin kenan, don haka ki saki jikinki Aisha so nake na baki wani dan bayani a game da layar dake wuyanki domin na ga kina cikin wahala da tsananin rayuwa."
Aisha ta dubi farar balbelar ta ce.
"Baiwar Allah, dan Allah ki yi hakuri ki barni na koma da baya zuwa cikin makaranta wallahi ban san cewa nan hanyarku bace da ba zan biyo ba."
"Kada ki ji tsoro Aisha ba laifi kika yi min ba, ina son kuma ki kwantar da hankalinki ki daukeni a matsayin uwa kamar yadda wani daga cikin kakaninki na can baya ya daukeni shekaru dari da ashirin da suka wuce." Balbelar ta ce tana mimmike dogon wuyanta.

"To, baiwar Allah yanzu me kike son yi dani kuma?" Aisha ta ce jikinta na kyarma.
"Abin da nake so dake Aisha shi ne idan kin je gida yau, ki shiga daki ke kadai sannan ki cire layar da ke makale a wuyanki ki warwareta domin akwai wani tsohon sako na kakanki na can baya ya barwa wani daga cikin yayansa, amma basu sami damar budawa ba domin sun dauka layar maganin tsautsayi ce. Abin da basu sani ba shi ne, layar ba maganin komai bace sakone aka rubuta a ciki tun tsawon shekaru dari da ashirin din da suka wuce sakon yana rufe har yau ba a sami wanda ya karanta sakon ba. To amma yau ina son ki warware layar ki karanta sakon da yake ciki domin arzikinki yana cikin layar a nannade."
Farar balbelar ta yi shiru tana duban Aisha wace hannayenta biyu ke dafe da layar da ke makale a wuyanta.
"Aisha na ga kamar kina shakkar abin da nake cewa. Ina son yanzun nan ki warware layar a gabana ki karanta koda sidira biyu ce domin ki tabbatar da abin da nake fada miki."
Cikin rawar jiki sai Aisha ta ciro layar dake wuyanta, ba wai dan ta yi imani da abin da balbelar ta fada ba, sai don a tunaninta idan taki bin umarnin aljanar mai siffar balbela za ta iya halakata. Cikin abin da bai fi mintuna biyu ba, Aisha ta warware layar da kyar tana gumi sannan a hankali kamar mai yin tiyata sai ta fara warware rubabbiyar takardar, ba a dade ba ta warware layar baki daya sannan ne to ta dubi wasikar cikin kaduwa da kuma mamaki.
Rubutun wasikar da AJAMI na Larabci aka yi shi bada rubutun Hausa ba. Aisha ta dago kai gumi sai zuba yake kamar ruwa. Aisha ta dubi balbelar ta kakkafa fiffike cikin lalaci.
"Karanta farkon wasikar Aisha kafin ki je gida ko kya dada gaskata ni." Aisha ta dawo da idanunta kan rubabbiyar takardar dake kokarin rabewa gida biyu, sannan ta kurawa kananan rubutun idanu. Ta fara karantawa kamar haka:
Daga sarkin barayi ZANGERU

Zuwa ga dana AMADI. Kafin in sanar da kai komai ina son ka sani cewa tun da nake a rayuwata ban taba tsinana wani abin kirki a rayuwata ba sai SATA!
"Ya isa haka nan." Balbelar ta katseta. Sannan sai ta yi girgiza, har sau uku. Wani dan kankanin dutse fari mulmulalle ya fado daga bakinta.
"Dauki wannan dutsen Aisha, na san nan ba da dadewa ba za ki bukaci ganina. Idan bukatar ganin nawa ta taso, sai ki murza dutsen har sau uku a tafin hannunki za ki ganni na bayyana."
Aisha ta durkusa ta dauki farin dutsen jikinta na rawa ta jefa shi cikin jaka, sannan sai ta dago kai zata dubi balbelar.
Gaban Aisha ya fadi, domin bata ga komai ba, ko sama ko kasa balbelar ta bace sai famfonan mai tsiyayar da ruwa.
"Mafarki nake yi?" Aisha ta ce muryarta na rawa, sannan sai ta leka cikin jakarta.
Har yanzu farin dutsen nan na nan.
***
Shafi'u ya kurkurda ta tsakanin tarin motocin cikin sauri ya nufi inda motarsa take, ya bude kofar motar kafafunsa a kasa ya zauna akan kujerar gaba ta motar sannan ya dubi agogo cikin damuwa.
"Me ya tsayar da Aisha ne?" ya tambayi kansa. Ko shakka ba ya yi lokacin tashinta ya yi, kuma ya tabbata ta nan Aisha zata zo wucewa.
Shafi'u ya lalubi aljihun wandonsa cikin damuwa ya dauko naira darin karshe da ta rage masa ya fara juyata a hannunsa, sannan sai ya shigar da kafarsa daya cikin motar ya jingina kansa da majinginin motar kana ya lumshe idanu yana kulle-kullen zuci, kulle-kullen da yake fatan su za su kai shi ga dora hannunsa a kan makudan kudin da yake fatan ya taimaki Aisha dasu.
Wannan saurayi Shafi'u dogone kyakkyawan gaske, wankan tarwada me kyawun fatar jiki, yana da tarin gashin gira, haka nan kuma yana da tarin gashin ka duguzunzum kamar kayar bushiya. Wata sa'ar idan ta rayawa Shafi'u sai ya runa gashin ya mayar dashi baki sidik. Wata

sa'ar kuwa sai ya mayar dashi fari fat kamar gashin tunkiya, wannan shi yasa da yawa daga cikin abokansa na gida da na jami'a suke kiransa da suna Sisko. Duk wannan bata dami Shafi'u ba, domin tun da aka haifeshi a duniya ya fara wayo akidar samarin Amurka ta shiga zuciyarsa. Ya sha cewa shi fa da akai shi Makkah ya yi sati guda wai gara a kaishi Amerika ya yi sa'a guda. Shafi'u Sisko ya sha bakin cikin jin cewa wai an taba zuwa dashi Amurka, amma a lokacin yana goye a bayan mahaifiyarsa, duka duka bai fi shekara guda ba a duniya...........

KUDI DA MACIJI - 22

.

Aisha ta girgiza kai cikin gaggawa sannan ta dubi kawayen ta dake can gefe guda tace
A'a na gode tare muke da wadancan
ba sai in dauke ku gaba daya ba.?
Aisha ta dada girgiza kai kayi hakuri wallahi mun gode sannan saita dan juya tace Sai gobe ko shafiu ya goge gumi ya dubeta zuciyarsa a karye yace a sanyaye to shi kenan Aisha Allah ya kiyaye daman so na ke kawai na ganki muyi sallama shiyasa nake ta jiran fitowar ki tun dazu. Koda ya fadi haka sai aisha taji tausayinsa ya kamata akaro na farko a dan takin lokacin sai zuciya tace da ita tsaya koda mintiuna biyar ne ki saurare shi can kuma sai wata zuciyar tace da ita ke rabu dashi sha sha sha yi tafiyarki kawai kada ki saurare shi Iblis ne so yake ya hure kunnuwanki me wannan dan karyar yagani ajikinki da har zaice wai yana kaunarki wannan ita tasa aisha juyawa bayanta tanufi inda kawayenta suke. Koda su aisha suka juya suka nufi gurin shiga motar sai aisha taji ajikinta cewar shafiu na nan inda ta barshi tsaye haryanzu yana kallonta duk da haka bata juyo ta kalle shi ba domin abin dayafi damun zuciyarta alokacin shine maganganun da Aljanar balbelar nan tayi mata da kuma mulmulallan dutsen nan data bata A tunanin Aisha gani takeyi kamar kowane lokaci daga yanzu mulmullen dutsen rikewa zaiyi ya zama wani Katon ALJANIN.

** ** ** **

Sa'ar da aisha ta isa gida saita wuce kai tsaye zuwa cikin dakinta sannan taja kofa ta rufe lokaci guda kuma tasa jakarta agaba ta kuma mata idanu bata ko kiftawa zuciyar ta na wasi wasi shin yanzu zan karasa karanta bayanin wasikar nan ne ko kuwa na bari saida tsakar dare aisha ta tambayi kanta duk kuwa da cewa tayi imani da bazata taba iya karanta wasikar layar da tsakar dare ba tunda dai ta shafi aljanu aisha ta godewa Allah domin lokacin data dawo daga makarantar uwar rikonta bata nan tafi unguwa dan haka babu kowa agidan daga ita sai tattabaru da kaji da kuma wata shegiyar akuya mai kukan tsiya wannan shi ya baiwa Aishat damar shiga daki ta kulle kanta aciki.

Tsahon lokaci tana nan zaune tayi tagumi wacce akayiwa mutuwa daga karshe dai sai ta yanke shawarar bari ta karasa karanta wasikar kada taki karantawa tayiwa Aljanar laifi cikin lalaci jikinta na rawa aisha ta lalubo takardar daga cikin jakarta amma bata yarda dutsen nan da aljanar ta bata yataba taba aisha ta warware wasikar sannan taci gaba da karantawa kamar haka.

.

......Aduk iya tsayin zamanin danayi ina sata ban tara komai ba da zan iya bar maka gado gashi kuma mutuwa ta rutsani adaidai lokacin danake dab da cimma nasarar sata ta karshe aduniya wacce daga ita ne nake sa ran yin bankwana da sata Amadi inason idan ka gama karanta wasikar nan ka bari sai bayan shekara biyu ka nufi katuwar fadamar nan ta DANMASU dake daf da gandun sarki kabi bangaren arewa zaka ga wata doguwar bishiyar giginya a daf da fadamar idan ka duba kadan daga arewa da bishiyar zakaga wani dan kwari mai kama da lalatacciyar kushewa

ina umartakar daka tono cikin ramin zaka sami duk irin dukiyar da kake bukata a zaman ka na duniya ina kuma gargadin ka da cewa da zarar ka dauki dukiyar kayi hanzari ka dauke mahaifiyarka TAGOGORI kubar garin domin zamanku na da

hadari matuka.
Nine mahaifinka ZANGERU.
.
Aisha tayi ajiyar zuciya sa'ar data kai karshen wasikar sannan saita sake dawowa da baya ta fara karantawa tun daga farko sannu ahankali har saida ta karanta wasikar sau goma sha uku amma bata fahimci komai aciki ba aisha ta share zazzafan gumin dataji ya fara sartu akan goshinta.
.
Ina umartar ka daka tona cikin ramin zaka samu duk irin dukiyar da kake bukata a zamanka na duniya.
.
Kalaman wasikar suka fado azuciyar Aisha shin wacce irin dukiya ce acikin ramin a binne kuma a ina ramin yake?
Shin haryanzu dukiyar tana cikin Ramin.
Wannan dama wasu sune irin tambayoyin da suka fara kai kawo acikin zuciyar Aisha haka nan kuma tasan duk duniya babu mai bata amsar tambayarta sai Aljanar Balbelar nan mai dogon wuya idan har akwai abinda aisha take tsoro shine tayi kiran balbelar tunanin mulmullen dutsen nan dake cikin jakarta ya fado mata.
.
Inason ki warware layar ki karanta sakon dake ciki domin arzikinki yana ciki.
.
Kalaman balbelar suka fara kai kawo acikin kwakwalwar Aisha shin da gaske arzikin nawa ne aciki ko dai Aljanar ce ke son wasa dani Aisha ta tambayi kanta acikin zuciyar ta ai kuwa balbelar tace daya daga cikin kakanninta ne ya rubuta sakon.
Aisha taci gaba da cewa cikin zuciyarta
.
Tunda nake ban taba tsinana wani abin kirki arayuwata ba sai SATA.
.
Aisha taji gabanta ya fadi sa'ar data tuno daya bangaren kalaman wasikar shin dukiyar da aka

binne din ta sata ce? Ta sake tambayar kanta.
Aisha na nan zaune cikin rudani zuciyarta kunshe da tambayoyi sama da tasbaha guda duk babu amsoshinsu har zuwa sa'ar dataji an kwankwasa kofar dakinta da karfi Ance.
Ke dan ubanki me kikeyi ke kadai acikin daki kamar Boka.
Marakiyarta ce keta banbanmin fadan wajen cikin sauri aisha ta dauke takardar wasikar ta cusa cikin jakarta sannan ta nufi kofar dakin ta bude a tsorace ta dubi......

KUDI DA MACIJI - 23

.

.

GORON SALLAH GA YAN UWA DA ABOKAN ARZIKI MASU BIBIYAR WANNAN LABARI NA

KUDI DA MACIJI

GORON SALLAR ZAI ZO AKALLA GUDA 4 KO 5 A WANNAN RANAR

.

Marikiyarta ce ke ta banbamin fada a waje cikin sauri aisha ta dauke takardar wasikar ta cusa acikin jakarta sannan ta nufi kofar dakin ta bude a tsorace ta dubi masifaffiyar uwar rikon nata.

.

Mama.....sannu da zuwa har kin dawo?
Eh na dawo me kikeyi ke kadai acikin dakin?
Zauna kenan daga makaranta shine na... Rufamin baki shegiya uwar gulma malalaciyar banza malalaciyar wofi shine wato tun da safe nace kizo ki wanke tsummokaran ki da kayan kikace saikin dawo daga makaranta shine kuma kika dawo kika shige daki abinki ko? To fitowa zakiyi yanzun nan sai kin wanke kayan gaba dayansu in ma bazaki wanke naki ba sai kin wanke nawa.
Ba'a fi mintuna biyar ba da faruwar hakan sai aisha ta fito zuwa tsakar gidan tafara wankin tsummokaran kayanta hawaye yana kwarara akan kumatunta sa'ar data dubi kayanta taga duk sun rube sun kokkode gashi kuma kala hudu ma kawai suka rage haka nan kuma babu ranar samun wasu tunanin mahaifanta ya fado mata azuciya duk da cewar sa'ar da suka mutu batafi

yar shekara bakwai aduniya ba amma haryanzu tana iya tuno zaman farin ciki tayi dasu a kuma mummunan hadarin daya kawo karshen rayuwarsu ya kuma kawo karshen duk wani farin ciki nata aduniya.

.

Shekara goma sha bakwai da suka wuce baya yarinya aisha tana gaban mahaifan cikin jin dadi da gata mara misaltuwa.

.

Mahaifanta Ahmed da saudatu bawasu masu hannu da shuni bane to amma suna da rufin asiri na zaman duniya mahaifin aisha malamin makaranta ne wanda bai dauki duniya da zafi ba haka nan bawan Allah ne nagari ma'abacon tasbihi ga ubangiji akusan kowane lokaci sa'ar dayake raye abokansa na kuruciya sunfi kiransa da A.A domin sunansa daya da mahaifinsa wanda shima sunansa Ahmad ayadda abokansa ke fadi ance wai kakansa ma sunansa Ahmadu acewar su wai sunan ya zamewa iyalin gidansu kamar gado kusan kowa sai ya sanyawa sunan dansa irin sunan mahaifinsa koda kuwa daga bangaren mace dan yafito.
Irin wannan al'ada ita tasa mahaifin Aisha addu'ar allah yabashi da namiji domin ya sanya masa sunan mahaifinsa kamar yadda shima akayi masa Allah mai yadda yaso sai yabashi diya mace wacce aka sanya mata sunan AISHA.
Wata safiyar talata da safe mahaifin aisha tare da ita sukayi shirin tafiya wani guri domin sadar da zumunci lokacin da suka fito zasu tafine to mahaifin aisha ya lalubi aljihunsa ya dauko wata laya ya mikawa Aisha ungo wannan layar rataya ta a wuyanki maganin tsautsayi ce in dai kina tare da wannan layar in Allah ya yarda babu abinda zai taba samunki na daga tsautsayi aisha ta karbi layar tana dariya ta rataya a wuya alokacin tana karama dan haka saita dinga murna don daman sa'ar da take ganin layar a wuyan mahaifinta tasha kokarin ta rabashi da iya yana Ki.
Baba wannan layar a kasuwa ka sayo min?

Mahaifin aisha ya fashe da dariya yadubi
mahaifiyarta saudatu kinajinmu da Aisha? Wai a
kasuwa na sayo mata wannan layar
saudatu ta dube shi da murmushi tace
Ina ruwan yar baba
mahaifin aisha ya dubeta da murmushi sannan ya
dafa kanta yace
wannan layar gado ce aisha nima mahaifiyata ce
ta bani ita tun ina karami kamarki ki riketa da
kyau kada ki jefar da ita kinji Aisha? Idan
wataran kin sami 'ya kema saiki bata.
Hakanan dayace da Aisha saiyasa lokacin da
suka shigo mota suka fara tafiya sai sukaga
maimakon aisha ta rataya layar a wuyanta saita
makalata a wuyan YAR TSANARTA mahaifan
aisha suka fashe da dariya
sha sha sha ba yar roba nake nufi ba mahaifinta
yace da ita cikin murmushi wannan shine ya
zamo murmushi na karshe da zaiyi agareta domin
awannan tafiyar ne kafin su kai garin da zasu
suka yi hadari babu wanda ya shura acikin motar
sai AISHA
An sami aisha agefen motar zaune da layarta a
wuya da yar tsanarta ahannu tana kuka Aisha
bata gaji wani abin kuzo ku gani agurin
mahaifanta ba inka dauke tsohon gidan mai
kamar makabarta da suke ciki sai tarin litattafai
da layar dake wuyan aisha gamida kudin
mahaifinta naira dubu uku da dari biyar aisha
bata gaji komai ba agurin mahaifan nata sai
hakuri da hankalinsu.
.
Bayan anyi sadakar bakwai sai HAJIYA KANDE
wacce kanwace agurin mahaifin aisha ta
bangaren uba haka nan kuma mace daya jal data
rage acikin yan uwansu na kurkusa ta dauki
Aisha.
Wannan mata Kande masifaffiya ce haka nan aka
haifeta da masifa kuma tanajin dadin masifa dan
ance wai sa'ar da tana budurwa a kullum sai
anyi fada sau goma da ita arana lokacin data
dauki aisha ta daukane akan dole ba don taso ba
sai dan tana gudun maganganun jama'a domin

ita kadaice mafi kusanci da aisha acikin danginsu da suka rage a doron kasa don haka tun ranar da aisha ta shiga hannunta tafara gallaza mata kullum saita jibgeta kamar ganga wata sa'ar ma har kan ruwan cikin aisha take hayewa tayita duka gata da nauyin tsiya kamar Alhaki ance sau biyu tana sumar da Aisha kafin ta zama budurwa. Aisha tana yar shekara goma sha biyar Kande ta sayar da tsohon gidan data gada.
Bazan iya wannan jaraba ba kullum sai na saya miki abinci gaki da cin tsiya kamar gara to ga gidanki nan na sayar kudin nake saya miki abinci da sutura da kuma....

KUDI DA MACIJI - 24

.

Bazan iya wannan jaraba ba kullum saina saya miki abinci gaki da cin tsiya kamar gara toh ga gidan ki nan na sayar kudin nake saya miki abinci da sutura da kuma daukar nauyin karatunki in ma kin cinye kudin ki ne.
Kande ce ke ta wannan masifar sa'ar data sayar da gidan sannu ahankali Kande ta cinye kudin Aisha kakaf.

.

Don haka ayanzu da aisha take durkushe tana wanki tana kuka tana tuna rayuwar da sukayi da mahaifanta bata da komai aduniya sai wannan layar dake wuyanta da kuma tsummokaran kayan ta kala biyar da Dankwali biyu duk ya kode yan tauye ya zama dan zarere kamar rawanin Maroki. Aisha ta mike tsaye daga kan kayan wankin ta goge hawayen dake sartu akan fuskarta koda aisha ta koma kan wankin saitaji ga mamakinta shafiu ya fado mata arai abin yabata mamaki me yiwuwa ko don ta fahimci ayanzu bata da wani mutum dake kaunar ta adoron kasa idan ba shi ba babu mamaki kuma kodon zuciyarta tana neman wanda zata fadawa sirrin dake cikinta sirrin da duk duniya babu wanda yasani daga Allah masanin komai sai Aisha saikuma Balbelar data bata labarin sirrin.

** ** ** **

Washegari da safe misalin karfe bakwai aisha

tafito sanye da kodadden kayanta masu kamar algarara dauke da jakarta a kafada zata tafi makaranta.
Lokacin data fito daga dakinta zuwa tsakar gida saita sami Kande zaune tana wanke wanke tana ganin aisha saita mike tsaye a fusace sannan idanunta suka kai ga wuyan Aisha
Dan Ubanki ina kika kai layar gadon taki?
Aisha ta sunkuyar da kai tace a sanyaye jiya ta fadi a makaranta.... Kafin aisha ta rufe baki ta kifeta da mari Tas Tas har sau biyu aisha ta rufe fuska hawaye ya fara sartu azuciyarta kuma tana cewa Wallahi ko kasheni zakiyi bazan baki labarin layar ba.
Shegiya tsinanniya wato saboda kin gama raina ni saida kika jefar da layar nan ko? Adaidai lokacin da wannan ke faruwa ne to wani dan siririn yaro mai kananan idanu ya shigo gidan wai ana kiran aisha a waje Kande ta dubi yaron cikin tsananin mamaki sannan ta dubi aisha domin tunda Aisha take wani saurayi bai taba kiranta ba musamman ma kuma yanzu da sassafe.
.
Jeka kace tana zuwa
kande tace da yaron azuciyarta kuma ta kudiri mugunta domin ta tabbata duk saurayin da zaiga aisha cikin wannan tsummokarar bazai kara sha'awar zuwa gurinta ba Kande ta juya ga aisha tace
Sai ki fata kiga wanda ke kiran wani asararrane shima da taya bera bari in banda sakarcin samarin zamani ma menene abin sha'aqa agurinki da har zaizo miki haka da sassafe aisha ta share hawaye batace komai ba saita juya ta nif kofar gidan itama zuciyarta cike da mamakin wanda yazo nemanta da sassafe haka kamar wadda tayi laifi da farko aisha tayi tsammanin ko wata kawarta ce dake nan makwabta wai ita SAFIYA to amma kuma idan Safiya ce ai shigowa zatayi ba turowa zatayi ba.
Aisha ta fita kofar gidan zuciyarta nata sake sake tana fita kofar gidan saitayi turus a zaune agaban

bakar mota marsandi kofarta a bude sanye da
shudin wando jeans da bakar riga damammiya a
kirjinta an rubuta 50 CENT kafafunsa sanye cikin
wani katon takalmi fari a mulmule kamar tamaula
gashin kansa bucu bucu ya rune shi fari fat
kamar gashin tunkiya idanunsa boye cikin bakin
tabarau SHAFI'U ne yake cin Cingam hannunsa
na hagu dauke da karan sigari tanacin wuta.
Kirjinsa na harbawa Das Das aisha ta matsa kusa
da kofar motar lokaci guda kuma tasa dan
yalolon gyalenta ta rufe hanci domin tuni warin
hayakin tabar ya fara shake mata makwogoro
shafiu ya lura da hakan cikin gaggawa ya jefar da
tabar waje yasa kasan takalminsa ya take.
Tunda bakya son warinta daga yau har abada na
daina shan taba Aisha
daka kyauta wa kanka aisha tace dashi cikin
damuwa tana dubansa
shafiu waya nuna maka gidanmu me kuma ya
kawo ka gidanmu? Shafiu ya dubi aisha cikin
damuwa yace
So da kauna ne yakawoni aisha zuwa gidanku
kuma tambaya nayi aka kawoni kinsan ance me
san tsuntsu shike binsa da jifa har cikin shekarsa
aisha tayi ajiyar zuciya ta sunkuyar dakai akwai
alamun damuwa karara a fuskarta
Shafiu ya dubi aisha sannan ya tausasa murya
bakiji dadin zuwana ba ko? Bakya kaunata ko
Aisha? Akwai alamun karaya karara a muryarsa
akaro na farko sai aisha ta dago kai ta dube shi
ta girgiza kai tace.
Ba kai bane bana so Shafiu ni irin dabi'unka ne
ke damuna shafiu ya dubeta sannan ya dubi
jikinsa cikin tsarguwa.
Dabi'una kamar wanne kenan? Fadamin su aisha
duk abinda bakya so wallahi nayi miki alkawarin
bazan sake yinsu ba har abada dama tuni na riga
nayi miki alkawarin daina shan taba ko?
Aisha ta dube shi cikin tausayi ko shakka batayi
ayanzu tasan da gaske shafiu yakeyi kaunarta
yake akwai wani abu a fuskarsa daya tabbatar
mata da hakan.
.

Dubi gashin kanka guduzumzum kalli faratan
hannunka zako zako kamar aljani fatar bakinka
har dani jan baki dubi irin wannan kwandalelen
zobe dake hannunka shafiu
Aisha tayi shiru shafiu ya shafa duguzumzum din
gashin kansa yace
Idan duk na rabu da wadannan abubuwa zaki iya
kaunata Aisha ?
.
BAKWAI. 7
Tsahon lokaci matasan biyun suna nan agurin
daya a zaune daya a tsaye kawunansu a
sunkuye...
KUDI DA MACIJI - 25
.
Tsahon lokaci matasan biyu suna nan agurin
daya a zaune daya atsaye kawunansu a sunkuye
wannan shine karo na farko da shafiu ya farajin
kunyar wata diya mace aduniya.
.
Bakice komai ba, aisha tayi ajiyar azuciya ta dago
kai ta dube shi akaikaice tace
Yanzu saboda ni duk saika daina wadannan
abubuwan shafiu?
Shafiu ya buga katon takalminsa daya akasa
yace duk abinda kike so na bari fadamin shi Aisha
wallahi nayi miki alkawarin zan bari saboda ke
indai zaki kaunace ni
Aisha ta sunkuyar dakai kasa na dan lokaci
sannan tace a sanyaye
kana Kaunata shafiu? Shafiu ya dubeta cikin
tsananin mamaki yace
saidai inso kike na maimaita miki amma ina
tsammanin aina fadi kalmar ina kaunarki tafi sau
dari tun farkon haduwarmu dake Aisha ta dada
yin ajiyar zuciya akaro na biyu
indai da gaske ne kana sona shafiu ina son ka
kudure aranka da kyakkyawar niyya cewa daga
yau ka daina duk wata muguwar dabi'a dabata
cikin addini amma saboda Allah badan ni ba
shafiu ya dubeta a rude
Ban fahimceki ba aisha
Abin da nake nufi shine ka nutsu kabar mugayen

dabi'a na sabon Allah ka kuma bari don Allah ba
don ni ba kaga sai Allah yabani ladan sanadin
shiriyarka da nayi shafiu ya kurawa aisha idanu
na tsawon lokaci sannan yace
Na fahimceki aisha in Allah ya yarda daga yau
zaki fara ganin canji acikin al'amaruna daga yau
din nan aisha ta dube shi da wani irin yanayi a
fuskar ta mai kamar murmushi tace
Amma danaji dadi shafiu
na fiki jin dadi aisha.
Tunda har nayi abinda ya faranta zuciyarki a karo
na farko ya danyi shiru sannan ai ya dubeta yace
Aisha ina son kiyimin wata alfarma.
Aisha ta dubeshi tace Alfarmar me kuma ni zan
iyayi maka?
Shafiu yace so nake kiyimin abinda ban taba
ganinsa a fuskarki ba Aisha ta dube shi a rude
Menene kuwa wannan abu?
Murmushi nake nufi Aisha tayi sauri ta rufe
idanunta sannan sai wani tattausan murmushi ya
subuce mata shafiu yaji wani dadi ya lullube
masa zuciya.
Daman zanfito kenan ka aiko yaro.
Shafiu ya janyo wata katuwar jaka dake kusa
dashi agaban motar ya ajiyeta akusa da kafar
aisha
mika wannan jakar cikin gida saikizo mu tafi
kinga mun kusan makara aisha ta dubi shafiu
cikin kaduwa sannan ta dubi jakar.
Shafiu wannan kuma jakar ta mecece? Shafiu yayi
murmushi
Atamfofi ne guda uku kawai da leshi guda biyu da
takalma kafa biyar kiyi hakuri aisha banida kudine
shiyasa ban sayo miki dan kwali da turare ba
aisha nta dubeshi cikin kaduwa ta girgiza kai.
.
Ina haba shafiu wannan kayan ai sunyi yawa ka
gan..... Shafiu ya daga mata hannu yace haba
Aisha kefa USTAZIYYA CE kinsan babu me mayar
da hannun kyauta baya sai shaidan Aisha ta
sunkuyar da kai shafiu ya fashe da dariya yace
Na daureki ko Ustaziyya Aisha?
** ** ** ** **

Tun karfe uku shafiu ya gama daukar darasinsa yana fitowa daga dakin karatun bai tsaya kama tasha ba kamar yadda ya saba sai ya wuce kai tsaye zuwa cikin motarsa ya zurawa hanya idanu yana jiran fitowar Aisha.
Karfe hudu da yan mintuna aisha ta fito tun daga nesa shafiu ya hangota hakanan ma aisha ma ta hango shi.
Shafiu ya daga mata hannu aisha ta nufi motar shafiu
sannu da zuwa aisha yaya lacka din?
Aisha tayi murmushi mun gode Allah shigo daga ciki mana ko kunya kikeji nasan halinku ustazan nan Aisha tayi dariya lokaci guda kuma ta bude kofar motar kusan duk a tsorace ta zauna kusa dashi amma kafafunta na waje
kaima ai yanzu ka zama ustazun aisha tace tana dariya shafiu ya fashe da dariya
Aisha ta dubi shafiu da murmushi tace
Kayi sallar la'asar kuwa? Shafiu ya girgiza kai wallahi banyi ba yadanyi shiru
Yakamata ka daina barin lokacin sallah yana wucewa gara ka dauke kanayinta akan lokaci shafiu ya sunkuyar da kai ga mamakinsa sai ya sami kansa yana mai kunyar hada idanu da ita.
.
In Allah ya yarda daga yau na daina bari sallah na wuceni Aisha ta dubeshi da murmushi tace wallahi kuwa daka burgeni shafiu ya dubeta cikin murna
Jin dadinki aisha shine farin cikina aisha ta lumshe idanu
ina fatan dai Sallar la'asar din ce kawai bakayi ba ko harda azahar ma?
Shafiu ya danyi jim sannan sai yace
Gaskiya bazanyi miki karya ba aisha rabona da salla tun asuba amma in Allah ya yarda aga yanzu....
Aisha ta katseshi gami dayi masa murmushi cikin wasa
Ah gaskiya tashi kaje kayi salla ka dawo kafin ta rufe bakinta shafiu yafito daga motar ya rufe kofar sannan saiya leka ta cikin tagar motar yace

Bari naje nayi sallar amma zakiyi kirana acikin
motar ko? Aisha ta gyada kai gamida juya masa
fararen idanunta ta gyara zama
Je Ka dawo (My One) Ina nan ina jiranka
.
My One shafiu ya nanata kalmar cikin zuciyarsa
ransa yayi dadi tunda yake wata mace bata taba
cewa dashi haka ba saidai ko shi yayi kokarin
fada musu hakan idan yana kokarin yaudarar su.
Shafiu ya ruga cikin sauri ya nufi Masallaci
.
Harkayi me?
Har nayi sallolin aisha ta rike baki
Kai shafiu wannan sallar taka da sauri take
CONCORD yanzu harka gama sallolin biyu?
Shafiu ya dubeta yace
Sauri....sauri nayi nagama aisha bana son na
barki kina ta jirana Aisha ta girgiza kai Idan ana
sallah...
KUDI DA MACIJI - 26
.
Idan ana sallah shafiu ba a tunanin kowa sai
Allah kuma nutsuwa ake bukata
ta danyi shiru sannan saitaci gaba da cewa
kamata yayi ka sayi yan litattafai na karatun
addini ka koma makaranta koka san Allah da
kuma yadda ake bauta masa shafiu ya gyada kai
idan na mayar dake gida saiki rubuto min
sunayen litattafan da yakama na saya dama
akwai wani malami anan bayan gidanmu saina
fara zuwa gurinsa da daddare
Yawwa shafiu ko kaifa aisha tace dashi sannan
sai idanunta suka kai ga rukuni balbelu dake
wucewa su takwas a sararin samaniya nan da
nan taji gabanta ya fadi Ras
(ARZIKIN KI YANA CIKIN WANNAN LAYAR)
Kalmar aljanar balbelar ya fadowa aisha
lafiya naga duk kamanninki sun sauya? Shafiu ya
tambayeta yana kallon canjin yanayin fuskar ta
cikin mamaki.
Babu komai Aisha tace dashi gamida murmushin
yake tuni har gumi ya fara sartu kyakkyawar
fuskarta me sheki kamar madubi arana shafiu ya

dada dubanta ya girgiza kai yace.
Kada kiyimin haka kefa ustaziyya ce bai kamata kiyimin karya ba abinda baki sani ba shine duk da gurbacewar tarbiyar nan tawa da kike gani Allah ya hore min wata baiwa in dai har mutum yafada min karya dana duba fuskarsa nake ganewa musamman MATA sanin kanki ne aisha ni kwararre ne a fagen mata duk da cewa dai ke kin zama daban kin sami nasara akaina amma hakan ba zai hanani na gane karya daga bakin abar da nake kauna fiyeda komai a duniya ba Shafiu yayi shiru aisha ma ta yi shiru ta sunkuyar da kai
Minti guda da yan dakiku suka shafe babu wanda yace da wani Kala
Kada ki damu Aisha idan bakya son kifada min abinda ke damunki shikenan bana son wannan ta zamo sanadiyyar bacin farin cikin rayuwata Aisha ta dago kai cikin cikin sauri tace.
.
Kayi hakuri shafiu kada kayi fushi dani....shafiu ya saki murmushi yake duk kuwa da cewa ransa ya sosu
ban taba yin fushi dake ba aisha kece me sa fushina ma ya dawo farin ciki aisha tayi ajiyar zuciya.
Fada masa kawai.
Wata zuciya ta fara yi mata kururwa shi kadaine me kaunarki aduniya kinsan kuwa babu wanda ake sirri dashi sai masoyi aisha ta dubi shafiu tace
Shafiu jiya kace kana son na baka labarin layar nan daka gani awuyana shin haryanzu kana son jin labarin layar tawa.?
** ** ** **
Wata jibgegiyar budurwa fara jau ta sheke da dariya sautin muryarta kamar bindiga tace Allah ya kiyaye na auri Tsololo kamar ka cab. Dube ka fa saikace Lawurje jiki duk ba nama.
Dan tsololon saurayin dake tsaye gabanta sanye da wani kwabdeden tabarau fari ya dubi budurwar da murmushin yake duk kuwa da cewa muzantashi din datayi yayi matukar kona masa zuciya

To ke in banda lalacewar zamani ma ina ni ina zabiya abinda baki sani ba shine nifa jibgegiyar mace irin ki ba kalata bace gaku da cin tsiya kume ke yanzu in banda anayi miki alkunya ma kullum fa sai kinyi tusa sau saba'in acikin aji sai Kace BODARA
Wasu samari acan gefe guda suka tuntsire da dariya har da shewa.
Shafiu yaso yabi sahunsu wajen kyakyatawa to amma labarin layar da aisha ta gama bashi ya cire duk wani nishadi dake cikin zuciyarsa domin tun kafin ta gama bashi labarin yafara gumi musamman ma sa'ar daya fahimci cewa maganar dukiya ce a binne a cikin kasa duk da cewa dai labarin Da aisha ta bashi yafi kama da almara amma shafiu bai daina keta gumi ba.
Cabdin dukiya abinne?
Shin da gaskene gwala gwalai ne? Ko kuwa zinariya ce me yiwuwa ma.
.
Tunanin me kake naga kayi shiru?
Aisha ta tambaye shi sa'ar dataga tun data gama bashi labarin baice Uffan ba Shafiu yayi ajiyar zuciya sannan ya dago kai ya dubeta akaro na farko tun bayan da tagama bashi labarin.
Kina nufin kice min layar dake wuyanki shekararta dari da shirin 120yrs ?
Aisha ta dubeshi cikin damuwa
Nima fa balbelar ce ta fadamin ta danyi shiru daman nasan da wahala ma ka yarda domin abin yafi kama da tatsuniya in ban da naga kamar ranka ya baci ma da bazan baka labarin ba ina ganin mu bar zancen kawai musa soyayyarmu agaba kaji shafiu?
Shafiu ya girgiza kai yana kallon sararin samaniya ta cikin gilashin gaban motar amma a zahiri ba gilashin yake kallo ba kwakwalwarsa ce ke kai kawo.
Bazamu bar zancen nan ba aisha kinajin abinda tace dake fa
ARZIKIN KI NA BINNE ACIKI waya sani ma ko lu'u lu'u ne aciki kin ko riga kinsan yadda suke da matukar daraja awannan zamanin idan har

kika same su mun gama warkewa aisha.
Aisha ta dubi shafiu cikin mamaki
kana nufin kace dani ka gaskatani labarin dana baka? Shafiu ya dubi aisha fuskarsa a murtuke yace shigo da kafafunki cikin motar ki rufe kofar aisha taso tayi gardamar yin hakan to saidai abinda ta gani a fuskarsa shi ya gargadeta cikin sauri ta janyo kofar motar ta rufe
Takardar da kika baro daga cikin layar tana ina?
Aisha ta dubeshi a rude tace Gata nan acikin jakata
Daukota mu gani Aisha ta bude jakar hannunta na rawa ta mika rubabbiyar takardar sannan ta dauko sauran kwanson fatar layar data barke ta dora masa a cinya shafiu ya warware takardar ahankali ya kurawa rubutun ajamin idanu na tsayin lokaci shafiu ya tsinewa jahilci a karo na farko arayuwarsa domin bai iya karatun ajami ba cikin takaici..

KUDI DA MACIJI - 27

.

Shafiu ya tsinewa jahilci akaro na farko arayuwarsa domin bai iya karatun ajami ba cikin takaici ya mikawa aisha yace a tausashe.

.

Sake karanta mana abinda ke ciki meyiwuwa mu dan fahimci wani abu daga ciki Aisha ta dubeshi da murmushi tace
Anya kuwa akwai abinda zamu iya fahimta aciki?
Shekara dari da shirin fa ni dai sau goma sha biyu ina karantawa ban fahimci komai aciki ba yanzu haka ma ba anan garin aka binne akwatin ba ni dai aganina wannan duk shirme ne irin na Aljanu ba gaskiya bane shafiu ya girgiza kai gamida dada mika mata takardar.
Gaskiya ne aisha jikina ya bani hakan domin bai kamata da kika buda kiga sakon rubutun aciki ba inda karyane duk da yake dai nasan.... Ya danyi shiru.
Ke dai sake karanta mana bi ahankali kadan kadan me yiwuwa ma tashi ma tsinci dami a kala aisha ta dube shi na dan lokaci sannan saita zunkuda kafada ta saduda ta fara karanta

wasikar mai rubutun ajami.
Shafiu yayi fakare baya ko kwakkwaran numfashi yana sauraron Aisha.
(KABI FADAMAR NAN TA DAN MASU DAKE DAF DA GANDUN SARKI KABI BANGAREN AREWA)
Dan tsaya haka aisha. Shafiu ya tsayar da ita cikin gaggawa aisha ta dago kai daga kan takardar ta dube shi
Me yafaru? Shafiu ya nuna takardar da hannu yace
Fadamar wa ma kikace? Sake karanto gurin Aisha ta sake kurawa takardar idanu sannan saita daga kai tace.
FADAMAR DAN MASU.
Shafiu ya dubi aisha cikin doki yace.
Haryanzu baki fahimci komai ba? Aisha ta gyada kai cikin damuwa haba aisha Dan Masu fa duk garin nan wanene bai san DAN MASU HOTEL ba? Aisha taji zuciyarta ta harba cikin sauri tace.
Fadamar dan masu fa akace ba Otal ba shafiu ya matso dab da aisha cikin doki yace da ita a tausashe
Abinda baki sani ba shine otal din abakin katon dam din nan na dan masu aka ginata shin ke baki taba zuwa bane? Aisha ta girgiza kai sau daya aka taba gayyatata liyafar bikin wata kawata danaji an ambaci otal nace bazani ba shafiu ya shafi dugunzunzum din gashin kansa da hannu yace
saurara da kyau kiji Aisha wannan Otal din danake baki labari gurin zuwana ne tafiyar kilomita goma sha biyar ce daga nan mun sha zuwa PARTY da yan mata akwai wani abokina dake aiki a otal din sunansa USMAN TASKA ya taba cewa dani asalin wannan dam din na Danmasu wata katuwar fadamace aka mayar da ita dam shafiu ya danyi shiru sannan sai ya daki kan sitiyarin motar da karfi cikin doki.
Meye haka? Aisha ta tambaya atsorace
aisha inajin Allah fa yakawo arzikinmu shin kin taba sanin Inda gandun sarki yake kuwa? Aisha ta girgiza kai
Nifa kifin rijiya ce babu inda nake zuwa.

To bari in fada miki tsakanin gandun sarki da danmasu dam baifi daga nan din nan da muke ba zuwa dakunan kwanan mata aisha ta dube shi cikin kaduwa.
Kana nufin kace dani anan aka binne akwatin shafiu ya gyada kai yace Ko shakka ko shakka banayi Aisha amma dai ki bari yau din nan in dare yayi zan tafi otal din na sami abokina usman taska zan so na karewa bakin dam din kallo me yiwuwa ma har zuwa Gandun sarkin.
Aisha ta dubi shafiu da murmushi kai shafiu da son duniya kake dubi duk yadda kabi ka tsatstsara abin nan kamar da gaske Shafiu ya bata rai ya dubi aisha
Aisha wallahi abinda nake fada miki ya wuce wasa kada kiyi mamaki nan da sati guda mun gama shigowar gari aisha ta fashe da dariya.
Allah yasa shafiu ya dubeta cikin murmushi yace Zaki iya bar min takardar nan agurina zuwa gobe? Aisha ta gyada kai riketa ma nan da wata daya ka dawo da ita
bana fatan sati guda ma ya wuce ban gano inda dukiyar nan take boye ba y danyi shiru sannan sai ya dubi aisha da murmushi
idan dukiyar nan tazo hannunmu dame dame zaki saya ma'ana me zakiyi da kudaden? Aisha ta sake fashewa da dariya tace Oh na shiga uku wannan fa shine zakin mazallako wai 'Da daga ciki yana rokon uba kwabo tun kafin dukiyar tazo tun kafin ma kayi tunanin inda zaka sayar harka fata kasafi shafiu ya dubeta cikin dariya.
Haba aisha ai dillalin wada shiyasan kudin jariri ke dai a sami kudiyar ai sayarwa ba aikibane agurina ya danyi shiru
Duk da haka dai ya kamata ki fara kasafin abinda zakiyi da kudin kinga da sunzo hannu shikenan sai Yi aisha ta sake fashewa da dariya domin ita harga Allah bata taba kawowa aranar za'a sami wata dukiya binne a kasa ba to amma gudun kada yaga kamar bata goyon bayansa saita dubeshi tace cikin dariya.
To ni yanzu shafiu idan na sami wadannan kudade masu dimbin yawa me zanyi dasu ne?

Shafiu ya wangame baki cikin kaduwa da mamaki yace
Me zakiyi dasu fa kikace? Haba aisha ai KUDI DA MACIJI MAGANINSU KASHEWA.
Aisha ta fashe da dariya Allah nuna mana ranar kashe su.
Shafiu ya lumshe idanu cikin farin ciki Yace Ameen Ameen Aishata.
** ** ** **
Karfe tara saura kwata daidai ya karaso Danmasu hotel zuciyar nata sake sake da zane zane idan banda nufin Allah ma da tun a hanya zaiyi hadari domin sau uku manyan motoci suna auna shi dan ko kusa ko alama tukin kawai shafiu yakeyi amma hankalinsa baya kan motar haka nan duk kusan minti biyu sai ya shafi aljihunsa ya tabbatar tana nan domin ga shafiu takardar tamkar Cek din milliyar dubu take. Shafiu...
KUDI DA MACIJI - 28
.
Domin ga shafiu takardar tamkar cek din milliyar dubu take.
.
Shafii yayi mamaki sa'ar da yayi fakin da motarsa ya nufi farfajiyar otal din ba wani abune sashi mamaki ba sai ganin babu kowa a farfajiyar otal din ko ina ka duba a bushe kamar makabarta sai jifa jifan ma'aikatan otal din nan da sunan sunturi
Shafiu ya nufi dakin tarbar baki na otal din kenan sai ya hangi usman taska shi kadai yana zaune akan kujerar roba ya jingina da bishiyar dabino tsinken tsire a hannunsa na dama ha nan hannunsa na hagu na rike da sigari yana ta karawa sararin samaniya hazo abinda idan ka dube shi da kyau alokacin saika rantse da Allah babu abinda ke damunsa aduniya nan kuwa idan da za'a rutsa shi ko naman jikinsa za'a saya ba zai biya kudin bashin da ake binsa ba.
Shegen sama me ya kawoka haka yau tunda wurwuri naga kuma kamar ma kai kadai ne ba joni ko?
Usman taska ne ke magana shafiu ya matsa kusa

dashi suka tafa sannan ya zauna akan wani
katon dutse fari dake kusa da bishiyar dabinon ya
dubi Usman taska yace.
.
Me yafaru ne naga Otal din naku haka So Dry
kamar an share naga kuma banji hayaniyar yan
duniya agurin wanka ba Usman taska yayi
murmushi yace.
Yaushe rabon ka da otal din nan ne?
Shafiu ya dan karkata kai gefe kamar zakara yana
tunani
nafi sati guda rabona da nan kasan ni yanzu
nafara girma aure ma nake son yi na huta kune
dai kullum jiya ya yau ba kwa girma usman ya
fashe da dariya yace.
Haba shafiu girma dai ai mun riga munyi shi tun
da dai ba haka aka haife mu ba saidai ko
HANKALI ya danyi shiru yana kyakyata dariya
wacce lalatacciyar ce zata yarda ta aureka shafiu
ya dubi usman da murmushi.
.
Yanzu dai ni ba wannan bace ta kawo ni tashi
zakayi mu dan zagaya zuwa can bakin dam gurin
yan wanka saika bani labarin abinda ke faruwa
din cikin sauri usman taska ya mike tsaye daman
wallahi nagaji da zama gashi kuma yau Otal din
babu kowa duk sai gundura.
Suka fara tafiya ahankali zuwa bakin katon dam
din dake fuskantar otal din daga inda suke suna
iya hango ruwan dam din yana tambal tambal
abin gwanin ban sha'awa gashi kuma bishiyoyi da
sukayi sahu sahu abakin dam din duk anbisu da
kananan kwaya kwayen lantarki saisi sukeyi
kamar rana hakan shi ya baiwa ruwan dam din
launin tsanwa tsanwa shudi shudi idan ka
hangeshi daga nesa.
Wai me yake faruwa ne usman? Shafiu ya
tambayi usman ya busa hayakin sigarinsa sama
sannan ya yagi dunkulen nama daga jikin tsinken
tsiren ya fara tauna cakam cakam kamar me cin
cingam.
Wasu yan iska ne wallahi sukazo daga cikin gari
zasuyi fati kawai sai suka kaure da fada har an

kashe mutum uku kuma abin haushi wai duk akan wata Bebi.
An kashe mutum ? Shafiu ya tambaya cikin kaduwa
an kuma raunata mutum ashirin bashiyasa ai kaga bakin ruwan ba kowa tun jiya yan sanda suke kame har mutum abin ya tabamu har an kama mutuniyata ma MONIKA shafiu ya fashe da dariya.
Saika tafi beli usman ya girgiza kai yace Allah sawwaka kai nifa yanzu wallahi so ma nake na tuba na koma ga Allah wadannan al'amuran duk sun fara isata domin na fahimci kamar duk babu riba
Da ka kyautawa kanka wallahi shafiu yace.
Koni nan ma da kake ganina na tuba wata yarinya na samu ustaziyya mai yawan wa'azi duk ta karyamin gwiwa wallahi.
Usman ya fashe da dariya yace
Uhm.. Uhm fa shafiu kada kayi tuban muzuru.
Allah ya sauwake shafiu yace gamida murtuke fuska ganin hakan sai usman yayi shiru sukaci gaba da tafiya zugum zugum abakin dam din.
.
Wai ina zamu ne? Usman ya tambaya sa'ar da yaga tafiyar tayi nisa har sun fara tunkarar Gandun sarki
Akwai abinda nake son nagani kasan kwana biyu ban zagaya bakin dam din nan ba sukaci gaba da tafiya sannu ahankali har suka kawo daf da wasu manya manyan bututu na ruwa an tara su jibgi guda abakin dam din.
Wadannan kuma bututun na menene?
Shafiu ya tambaya lokaci guda kuma yana kallon katon ramin mai mai tsayin gaske dake gabansu tuni har an fara binne wasu daga cikin bututun ruwan acikin dogon ramin.
Kamfanin ruwa ne ke kokarin kafa wasu manya manyan injinansu wadanda zasu ringa tura isashshen ruwa cikin gari da tuni ma aikin yayi nisa in badan ma'aikatan dake haka sun tarar da dutse ba shafiu ya dubi usman cikin mamaki dutse fa kace ainaga duk fadin dam din nan babu

wani babban dutse ballantana ma har a sami
wani dutse a karkashin kasa.
Usman ya zuki guntuwar tabar dake hannunsa ya
jefa sauran cikin ruwa.
Abinda yayi ta baiwa mutane mamaki kenan
yanzu kokarin da akeyi shine a kokarta fasa
dutsen idan kuma ba zai fasu ba sai a karkata
ramin yabi ta wata hanyar daban shafiu yayi
shiru yana saurаron usman da ace rana ne babu
abinda zai hana usman ganin fuskar shafiu jike
shakaf da gumi hakanan bugun zuciyarsa ya karu
akan na da.
.
Adaidai inane aka sami dutsen usman ya dubi
usman shafiu yace Ga ramin nan abayanka kusa
da BISHIYAR GIGINYAR CAN shafiu yaji yawun
bakinsa ya kafe cikin sauri ya dubi usman taska
yace
Ko zan sami cocila a otal dinnan naku?
Usman ya dubi shafiu ya girgiza kai kaifa baka
rabuwa.......
KUDI DA MACIJI - 29
.
Kaifa Baka Rabuwa da rigima me kuma zakayi da
cocilar? Shafiu yayi masa murmushi yace
'Ka dauka kai kaine taska makunshin labarai? So
nake nima naga dutsen da idanuna yana rufe baki
sai ya nufi ramin cikin sauri ya gangara ciki
idan ka gama tsurkun ka sameni anan usman
yace sannan sai ya kunnawa sabuwar sigari wuta
ya zauna akan yashi ya zurawa ruwan dam din
idanu yana tambal tambal
Shafiu na shiga cikin ramin sai yaji ya taka wani
abu mai taurin tsiya kamar dutse jikinsa na rawa
ya lalubi aljihunsa ya zaro wayar salularsa
sannan ya danna wani madanni nan da nan
haske yazo a fuskar wuyar salular tsahon lokaci
shafiu yana nazarin abin ko shakka babu abin
yaso yayi kama da dutse amma shafiu ya tabbata
ba dutse bane domin tun sa'ar da kafafunsa suka
dirga akan abin yaji sautin baiyi kama da na
dutse ba.
To amma saboda ya matsu daya tabbatar da

abinda yake zargi sai wata dabara ta fado masa jikinsa na rawa ya fito daga cikin ramin yafara dube dube ba a dade ba ya hangi wani dan madaidaicin dutse ya buga akan abin da karfin gaske maimakon yaji sautin yabayar da KWAS. Sai yaji yabada wani DUM.. Nan da nan shafiu ya mike tsaye ko shakka bayayi abinda yake zargine dukiyar masoyiyarsa sa ce Aisha Allah ya nuna masa ita a saukake.

.

Usman ya mike tsaye gamida hamma sa'ar da shafiu ya nufo inda yake cikin sauri
harka gama tsurkun?
Shafiu bai bashi amsa ba sai yace
yaushe ne masu hakar ramin nan suke tunanin fasa dutsen? Usman ya fesa hayaki sama.
Me yiwuwa sai nan da sati guda kasan rigimar da akayi anan shekaranjiya tasa jami'an tsaro sun sa dokar tabaci anan harna tsawon sati guda kafin su gama bincike binciken su na Al'ada.
Kana nufin kace daga yanzu har zuwa sati guda ba'a son aga kowa agurin ? Usman ya gyada kai yace Koda da rana ne kuwa ballantana da daddare shafiu yaji yawun ya dada yin sallama daga bakinsa tuni har yafara tsammanin yazama milloniya wai gashi nan ma har yan maula sun zagaye shi yana ta bari da naira.
Samarin biyu sukayi cirko cirko na tsawon lokaci suna kallon juna can sai shafiu ya dubi doguwar bishiyar giginyar nan yace wai usman irin wannan bishiyar giginyar takanyi kamar shekara nawa aduniya kafin ta mutu? Usman ya busa hayaki sama acikin tsananin mamaki domin ya lura akwai wani abu a tattare da al'amarin shafiu.
Wani kakana ya taba cewa dani bishiyar giginya na iya kaiwa shekaru casa'in aduniya koma fiye da haka in har ba sareta akayi ba nan da nan shafiu yaji gumi ya fara sartu abayan rigarsa.
Shafiu me yafaru ne kaketayimin irin wadannan tambayoyi kamar wani dan sandan ciki? Shafiu yayi shiru bai amsa ba wai tunanin me kaketayi?
Shafiu ya juyo firgigit sannan sai ya dubi usman da murmushi yake yace.

Tunani nake ina ma ace bishiyar giginya tanada
yawan inuwa dana shukata a tsakar gidanmu.
.
TAKWAS 8
Haba Aisha kinsan dai ai ba zanyi miki karya ba wallahi saida na taba saman akwatin da hannuna na tabbata itace ke har bishiyar giginyar da aka fada aciki wasikar na gani Aisha tayi shiru tana sauraronsa cikin tsananin kaduwa ta fara fahimtar abinda take dauka amatsayin tatsuniya ne ke naman ya zama gaske.
Yanzu abu daya nake son kiyimin Aisha indai kikayi hakan na tabbata gobe iyanzu dukiyar tana hannunki Don ba'a jira lamarin kudi ba kuma a bata lokaci ko kankani
Me kake son nayi maka?
Shafiu ya danyi shiru sannan yace Ina dutsen da kikace Aljanar nan ta baki?
Aisha ta bude baki cikin kaduwa me zakayi dashi?
So nakeyi kiyi kiran ta mu tambayeta inda hakikanin akwatin nan take koma kara tabbatarwa domin in dai abindata fada gaskiyane yakamata tasan inda aka binne dukiyar taki.
Ko bahaka ba?
Aisha tayi shiru na tsawon lokaci tana kallon kofar gidansu alokacin karfe goma da rabi na dare domin shafiu na barin otal din gidansu Aisha ya wuce kai tsaye da yake uwar rikonta kande ta dauke daya daga cikin atamfofin da shafiu yabata ba'a sami wata matsala ba wajen fitowar aisha.
Abin mamaki kande ce ma turo ta da kanta.
Yi sauri ki fita mana sai wani nuku nuku kikeyi wannan yaro ai ya isa dan arziki wallahi ga shi daga zuwansa har ya fitar damu daga cikin tsummokara.
To aisha kefa nake jira kinyi shiru.
Aisha ta dubeshi a tsorace tace wallahi shafiu tsoron kiran Aljanar nan nakeyi kaga....
Shafiu ya ya daga mata hannu menene abin tsoron bayan tace bazata cutar da ke ba?
Aisha tayi batace komai ba.
In kuma kina ganin dai tsoron bazai barki kiyi

kiranta ba to kirawo ta mana yanzu tunda ina tare dake.

.

Aisha tayi ajiyar zuciya in dai kana tare dani bana tsoron komai shafiu bari na kirawota ta bude jakarta ta fara laluben farin dutsen abinda bata sani ba shine tuni cikin shafiu ya fara kugi domin shima a bala'in tsorace yake to amma da yake ransa yana kan dukiyar dake binne saiya dake zuciyarsa amma gumi tun daga goshinsa har zuwa kan babban dan yatsan kafarsa zuba yake. Aisha ta dauko dutsen daga cikin jakar ta dorashi akan tafin hannunta ta lumshe idanu sannan ahankali saita fara murza dutsen a tafin hannunta.

Shafiu yayi mutuwar tsohuwa ko kwakkwaran numfashi bayayi.

KUDI DA MACIJI - 30

.

Shafiu yayi mutuwar tsohuwa ko kwakkwaran numfashi bayayi.

.

Wata guguwa mai karfin gaske ta turnuke zagayen motar sannan sai sukaji motar ta fara girgiza kamar za'a dauke su sama tsawon lokaci ana girgiza motar sannan kwatsam sai balbelar ta bayyana a gaban motar.

Matasan biyu suka zura mata idanu cikin kaduwa Kada kuji tsorona ku tambayi duk abinda kuke so daman nasan zaki neme ni ta dubi Aisha.

San..nu da...zuwa aisha tace bakinta na rawa

Yawwa aisha yi sauri ki fadi abinda kike son fada ina BIRNIN SIN fa kuka kirawoni sauri nakeyi zan koma na baro yarana acan.

Aisha ta dubi shaiu sannan ta dubi balbelar cikin hali So...muke mu san inda aka binne akwatin.

Balbelar ta girgiza kafadunta sannan ta dubi shafiu tace Ramin daka shiga dazun nan anan akwatin take kasan akwai wani bawana dana ajiye shi yayi gadin akwatin yau shekara dari da shirin yana zaune agurin yana gadinta. Ko dazu ma saida ka taka shi baka ganshi ba.

Shafiu ya dubi aisha duk da yake a bala'in

tsorace yake saida ya daga mata gira to in bakuda wani abu kuma da kuke son tamaba ni zan tafi
Mun...gode Madalla sai kuma wani jikon Aisha tace bakinta na rawa.
Balbelar ta dubi shafiu tace idan Allah ya kaddara auranka da ita ka riketa da kyau yarinyar kirki ce sannan ta bace.
Matasan biyu sukayi ajiyar zuciya lokaci guda shafiu ne yafara magana to sai yaya kuma? Saiki shirya gobe warhaka muna can in Allah ya yarda ko sha biyun dare bazatayi mana acan ba zamu dawo da dukiyar
kana nufin har dani zamu tafi? Aisha ta tambaye shi a tsorace.
Shafiu ya fashe da dariya cikin farin ciki yace Haba Aisha kiyi amfani da hankalin ki mana ai idan bakya agurin akwatin bazata dauku ba don bana tsammanin karama ce maiyiwuwa mai nauyin tsiya ce.
Kuma ni me zan iyayi ina mace?
Shafiu ya dubeta kana ya matsa dab da ita har tanajin numfashinsa afuskar ta yace Bakiji abinda tace ba? Akwai wani bawanta dake gurin yana gadin akwatin shi zamu sa ya janyo mana akwatin daga karkashin kasa.
Aisha ta bude baki cikin kaduwa.
Shafiu kada fa son abin duniya yasa ka zarewa in banda abinka a ina zamu ganshi Aljani ne fa shafiu ya sake fashewa da dariya wannan shine dalilin daya nace dake zamu tafi idan munje bakin ramin saiki murza dan dutsenki idan balbelar ta bayyana saiki roketa alfarma tasa wannan bawan nata dake gadi agurin ya zaro mana akwatin ko kuwa ya kika gani?
Aisha ta dube shi da murmushin farin ciki adaidai lokacin ne to Aisha ta kula da kansa Kai shafiu yaushe ka aske wannan gashin naka?
Shafiu ya fashe da dariya sai yanzu ma kika lura?
Aisha bata iya bashi amsa ba saitaci gaba da kallonsa sama da kasa Alokacin ne ma ta lura ashe har zako zakon faratan dake hannunsa duk ya yanke.

Wallahi daka aske gashin saika zama kamar ba kai ba.
Shafiu yayi murmushi sai nayi muni ko?
Aisha ta girgiza kai tace haba dai ai haka ma wallahi kafi kyau inama ace ina iya kallon ka sosai batareda jin kunya ba
SUKA FASHE DA DARIYA.
** ** ** **
Washegari tun da asuba shafiu ya tashi yayi sallah. Wannan shine karo na farko acikin shekaru goma sha takwas da shafiu ya tashi sallah da suba rabonsa da sallah tun yana dan shekara goma aduniya alokacin bai gagari mahaifansa ba.
Mahaifin shafiu zaune a dakin shakatawa suna karin kumallo sai suka ga shafiu ya shigo falon ahankali kamar maiyin sanda mahaifan suka kura masa idanu cikin kaduwa domin sun san shafiu in har ba makaranta zashi ba babu abinda zai tashe shi da karfe takwas na safe.
Mahaifinsa ALHAJI SADIQ ya kalle shi sama da kasa cikin kaduwa domin ya lura da cewa dugunzunzum din gashin nan da yayi matukar tsana shafiu ya aske shi.
Ina kwananku shafiu ya gaishe su a durkushe Lafiya lau shafiu... Suka amsa baki daya cikin mamaki tsawon lokaci babu wanda yace kala can sai Alhaji sadik ya dubi dansa yace a sanyaye shafiu yau kuma shiriya ce Allah ya kawo ma?
Shafiu kansa a durkushe yace Eh baba.
Zuwa ma nayi na roke ku gafarar abinda nayi muku abaya. Nayi muku alkawarin daga yau nabar shirme da sakarci mahaifiyar shafiu ta fashe da kukan farin ciki Mun yafe maka shafiu.
Allah sadik ya tashi tsaye sannan ya dubi dansa cikin farin ciki Na godewa Allah daya shirya min kai kuma tunda Allah yasa shiriya tazo maka saika nemo wacce kake so ayi maka aure.
Shafiu ya dago kai cikin farin ciki yace Gobe in Allah ya kaimu zan zo muku da ita baba mahaifansa suka dubi juna sukayi murmushi toh ai shikenan shafiu kuma indai naga ka zarce ahaka zan mika ma ragamar harkokina

ahannunka duk da yake dai ba wani abu nake dashi kamar da ba amma In Allah yakaimu jibi za'ayimin wani tsohon biyan bashi na kusan naira Milliyan hudu da zarar an kawo min su kai zan Dankawa.
Wannan wani abu ne daga Allah lallai babu abinda yafi komai dadi aduniya irin bin hanya madaidaiciya shafiu yace cikin zuciyarsa duk da wannan alkawarin da akayi masa na wannan makudan kudi zuciyar shafiu bata daina tunanin dukiyar dake binne a karkashin kasa ba.
** ** ** **
Wani katon gyare yayi tsalle ya fada fuskar.
KUDI DA MACIJI - 31
.
Wani katon gyare yayi talle yafada faskeken kunnen daya daga cikin yansandan dake bobboye abayan bishiyoyin suna nazarin bakin ruwan.
.
Dansandan ya kaiwa kunnen mari katon gyaren ya tashi dansandan ya mari kunnensa a banza. Kai wannan masifa dayawa take dansandan yace cikin zuciyarsa sau dayawa yakan zargi kansa da kansa amatsayin mahaukaci domin wai in ba mahaukaci ba wane ne zai shiga aikin dansanda aikin da akullum bashida wata riba sai ta bakin jini kullum kana gadin jama'a da dukiyoyinsu sukuwa nabinku da tsinuwa.
Shekarunsa ashirin da biyu yana aikin dansanda amma haryanzu bai wuce sajan ba idan karshen shekarar yazo yake sa ran yin ritaya.
Wannan dansandan sunansa AUDU ada can baya yasha niyyar barin aikin dansandan amma sai wani abokinsa yace dashi Haba audu kada ka jahilci aikinka mana wannan aikin da kake rainawa fa babu abinda yafishi muhimmanci domin daku yansanda da malaman makaranta idan babu ku babu gari kaidai abinda zakayi kawai shine ka tsarkake zuciyarka ka nemi Halali acikin aikina sai Allah yabaka lada yakuma albarkaci aikin Amma zancen wai kabar aiki wannan duk bata taso ba.
Wannan kalami na abokinsa shi yasa audu kaiwa

har tsayin wannan lokaci yana aikin Dansanda daga inda Audu yake fake yana iya hango duhuwar sauran abokan aikinsa su bakwai duk a rabe dauke da bindigogi suna nazarin bakin ruwan
Audu na nan a makale zuciyarsa tana yi masa sake sake domin matarsa nada tsohon ciki kuma awatan zata haihu haka nan har izuwa wannan lokacin bai sayi koda buzu ba.
Audu ya lalubi aljihunsa ya zaro kwalin taba cikin damuwa.
Dan cin hancin ma da muke karba anyi mana bakin ciki gashi dai ba wani kyautata mana akeyi ba amma saboda bala'i kuma ance wai duk hancin wanda mukaci yakaimu Kara...
Tunanin audu ya katse adaidai lokacin daya hangi hasken fitilar mota ta nufi bakin dam din abinda yabashi mamaki domin tunda aka kawo su adaren jiya kimanin karfe goma sha biyun dare har zuwa yanzun nan basuga motsin wani mahaluki abakin ruwan ba. To me yakawo mota kuma?
Cikin sauri jikinsa na rawa audu ya fito daga inda yake labe bindigar dake hannunsa ta dada nauyi in har akwai abinda audu yaki jiki shine akaishi aikin da za'a iya yin bata kashi kullum addu'arsa itace Allah yasa yagama aikin dansanda ido biyu kafa biyu hannu biyu.
Kamar audu sauran yansandan ma sun ga zuwan motar don haka sai suka firfito daga inda suke make kamar yadda aka umarce su sukabi cikin duhun kamar aljanu suka nufi inda sukaga motar tayi.
.
Shafiu yafito daga cikin motar ya rufe sannan ya zagaya ya budewa aisha itama ta fito amma jikinta na rawa kamar mazari da za'a tsaga jikinta alokacin zaiyi wuya a sami wani digo na jini.
Shafiu ya zaro wata katuwar cocila sabuwa daga aljihunsa sannan ya haske cikin ramin lokaci guda kuma ya jiyo ya dubi aisha yace toh Aisha aiki ya rage naki ga ramin nan munzo Ya dada haska

mata cikin ramin da cocilan.
Aisha ta kurawa ramin idanu na tsawon lokaci har yanzun nan takasa imani da cewa wai shekaru dari da shirin da suka wani daga cikin kakanninta ya binne dukiya acikin wannan ramin. Kinga ma bishiyar giginyar da nake fada miki keda ganinta ai kinsan ta dade dubi fa saboda tsayi harta lankwashe kamar macijiya.
Aisha ta zubawa bishiyar idanu na yan dakiku sannan saita dawo da idanunta cikin Ramin.
Toh aisha yi maza kiyi kiranta koma koma gida da wuri naga sha dayan har ta gota Aisha ta sauke jakarta daga kafada sannan ta bude jakar shafiu ya matso kusa da ita cikin sauri ya haske cikin jakar da cocilan hannunta na rawa ta dauko dutsen sannan ta murza shi atafin hannunta Sabanin yadda sukayi tsammani guguwa zata tashi awurin awannan karon lokaci guda balbelar ta bayyana abakin ramin ta kada fiffike tace Ai ina nan kusa daku bama sai kinyi bayanin komai ba duk shawarar da kuka yanke jiya ina nan tare daku inajinku In banda abinku ai ni ma ina iya dauko muku akwatin don baku san irin kaunar da mahaifinku ya nuna min bane shiyasa kuma nayi masa alkawarin isar da duk wani sakon nasa.
.
Tana gama fadin maganar sai tayi girgiza nan da nan kamar budar ido sai kasar wurin ta fara tsagewa sannu ahankali sai sukaga akwatin ta babbako daga cikin kasa ita kadai kaikace raine da ita sannu ahankali ta sauka akusa da inda motarsu take.
Balbelar ta kada fuffukanta sannan ta dube su tace Shikenan kwadayinku ya kwanta?
Aisha da shafiu suka gyada kai lokaci a tsorace domin abinda suka gano yayi matukar girgiza su. To ni zan tafi sai kuma mun sake haduwa. Kafin kiftawa da bismilla ta bace. Shafiu ya dubi aisha. Aisha ta dubi shafiu jikinsu na rawa cikin sanda shafiu ya matsa kusa da akwatin ya dallara hasken cocilarsa kamar yadda yayi tsammani haka ya ganta to saidai bata kai girman dayayi tunani ba duk jikin akwatin jajur yake da tsatsa

tun da yake bai taba ganin irin akwatin ba ko da kuwa a hoto ne domin wannan akwatin a dunkule take sunduki sunduki.
Haka nan akwai wasu abubuwa masu kama da madauki ajikin akwatin har guri shida awannan lokacin ne to aisha tayi abinda ta baiwa shafiu mamaki......
KUDI DA MACIJI - 32
.
Hakanan akwai wasu abubuwa masu kama da madauki ajikin akwatin har guda shida awannan lokacin ne to Aisha tayi abinda ta baiwa shafiu mamaki domin yana tsaye akan akwatin sai yaga Aisha ta matsa kusa da akwatin ta durkusa sannan saita sa hannu ta dafa akwatin tsawon lokaci tana nan a durkushe duk da yake baya iya ganin idanunta amma jikinsa yabashi cewa kuka take yi.
Kukan me kikeyi Aisha?
Babu komai. Tace dashi bakinta na rawa sannan saita mike tsaye ta dube shi tace Tayaya zamu iya sa ta acikin mota?
Shafiu ya bude baki kenan zai amsa sai wata bushashshiyar murya daga cikin duhun tace da can lokacin da kukayi satar bakuyi tunanin hakan ba?
.
Aisha da shafiu suka juya a firgice sannan ne to sukayi ido biyu da yansandan kowannensu rike da bindiga suna zazazare idanu.
AISHA TA KWALLA IHU A RAZANE.
** ** ** **
Yansandan suka dubi juna a rude cikin tsananin mamaki sa'ar da Aisha ta gama basu labarinta. Lokacin da yansandan suka ritsa su sun yi niyyar tafiya dasu ofishin yansandan gaba dayansu har da akwatin to amma kukan da aisha tayi ta rafsawa a tsorace tana magiyar cewa abarta zatayi bayani shiyasa INSFETA ZAKARI ya amince sannan yasa yansandan suka kawo motarsu bakin ruwan aka jefa aisha da shafiu aciki sannan aka nemi dasuyi bayanin abinda sukeyi abakin ruwan da wannan uban daren kuma dasu fadi

inda suka samo akwatin in dai ba sato ta sukayi ba.
Don haka sa'ar da aisha tagama basu labarin sai sukaji abin kamar almara Insfekta Zakari ya harari aisha gamida buga mata tsawa yace Ke kada ki raina mana hankali yanzu ke kina nufin mu yarda da wannan tatsuniyar da kika fara mana?
Aisha ta fashe da kuka wallahi ba karya nakeyi ba ai ga akwatin nan gakuma takardar wasikar nan ma agurinsa ta nuna shafiu wanda ke zaune bayako motsi saboda tsabar tsoro duk da wayewarsa babu abinda yake matukar tsoro irin DANSANDA.
Yanzu idan nace inason naga ita takartdar da kakan naki yabaiwa aljanar tabaki zaki iya nuna mana? Insfekta zakari ya tambayeta cikin sauri.
Aisha ta dubi shafiu tace Basu takardar nan shafiu.
Jikinsa na rawa ya lalubo takardar daga aljihun wandonsa ya mikawa Insfekta zaka.
Insfekta Zakari ya zurawa rubutun ajamin idanu.
Dayake wani zamani daya wuce yataba karatun Allo rubutun ajamin bai wani bashi wahalar karatu sosai ba amma duk da haka da kyar a daddafe ya hada bakaken sannan ya karanta wa sauran yansandan A Fili.
Jami'an tsaron sukayi shiru na tsawon lokaci sa'ar da suka fahimce ashe akwatin dake nan dab dasu acike take da dukiyar Milyoyin Kudi.
Insfekta zakari yayi ajiyar zuciya sannan ya dubi Aisha da shafiu yace na yarda da abinda kuka fada amma fa hakan baya nufin bazamu iya cazar ku da laifi kwata kwata bane kunga dai kayan nan da kuka dauko suna da hadarin gaske tunda ko shima kakan naki dukiyar ba tasa bace sata yayi.
Saboda haka kinga dolene hukuma tayi bincike akai mai tsayin gaske kafin a gano wanda ya mallaki dukiyar nan tun tsawon shekaru dari da ashirin. Ya danyi shiru.
Aisha taci gaba da shishshikar kuka hakan ya daya gani yayi matukar faranta masa rai don haka sai yaci gaba da cewa amma duk da

wannan hadarin da kuke ciki idan kuna so zan iya
taimakon ku.
Aisha da shafiu suka dubi juna a tsorace
Muna....so suka amsa baki daya
Insfekta yayi gyaran murya yace to abinda nake
so daku shine kuyi gum da bakinku kada ku sake
wani yaji labarin akwatin nan sannan kuma zan
rike wannan wasikar agurina zamuci gaba da
bincike har zuwa lokacin da zamu gano mai
dukiyar ku kuma kuyimin alkawarin zakuyi shiru
da bakinku idan kukayi haka zan sallame ku
yanzun nan ku tafi gida idan kuka sake labari ya
riskemu cewa kun bada labarin acikin gari to
zamuyi muku kamun Yan Fashi kun yarda?
.
Cikin sauri su aisha suka gyada kai insfekta
zakari ya kunnewa sigari wuta cikin farin ciki
sannan ya lalubi aljihunsa ya dauko Albashinsa
cancakat da aka biya shi awannan ranar ya
mikawa Aisha yace ga wannan yan mata kya rage
bacin ran da zaki shiga nasan tuni kin gama
kasafin abinda zakiyi da dukiyar kakanki ko? To
hukuma bazamu amince da haka ba domin shima
ba nasa bane sata yayi da'ace wasikar ta nuna
cewa dukiyarsa ce to da babu abinda zai hanamu
baki kayanki.
Aisha ta karbi kudin a tsorace shafiu kuwa ji yake
kamar zuciyarsa zata fashe domin yanaji yana
gani an raba su da milyoyin kudi an basu dubun
naira
.
Ku tashi ku tafi ku kuma iya bakinku kunji?
Insfekta zakari ya umarce su
Jikinsu na rawa suka nufi marsandin shafiu har
suka shiga motar suka tafi babu wanda yace da
wani QALA
tafiyarsu keda sai Insfekta Zakari ya dubi sauran
yansandan ya fashe da dariya sannan yace to ku
saurara da kyau kuji yau Allah yakawo karshen
wahalar da muka dade muna sha shekara da
shekaru ina fatan kowa daga cikinku zai iya
bakinsa domin wannan wata kyautace daga Allah
ina ganin abinda ya dace kawai shine mu sa

bakin bindiga mu bude akwatin nan mu kasafta
dukiyar dake ciki kowa tasa ta fisshe shi ko kuwa
ya kuka gani? Kunsan dai ba aikin kama barayi
aka turo mu baki ruwan nan ba kwantar da
tarzoma muka zo

KUDI DA MACIJI - 33

.

Mu kasafta dukiyar dake ciki kowa tasa ta fisshe shi ko kuwa ya kuka gani? Kunsan dai ba aikin kama barayi aka turo mu bakin ruwan nan ba kwantar da tarzoma muka zo.

.

Audu ne yafara cewa haka za'ayi yallabai sannan sai sauran ma suka amsa baki daya mintuna biyar da faruwar hakan yan sanda suka sa bakin bindiga suka balle daddiyar akwatin yar shekara dari da ashirin a karkashin kasa.

.

Insfekta zakari yakoma cikin mota ya dauko cocila sa'ar da aka bude tsohuwar akwatin yansandan guda takwas suka zagaye ta kowa na hadiyar yawu zasu kwashi banza daga inda suke tsaye suna iya hangen wasu abubuwa manya manya acikin akwatin.

Koda Insfekta zakari yataho dauke da cocilan sai yansandan suka dada marmatsawa domin su ga zinare da lu'u lu'un dake ciki Insfekta zakari ya haske cikin akwatin nan da nan yansandan suka dauke Numfashi lokaci guda cikin kaduwa da abinda suka gani.

Insfekta zakari yaji kamar hanjinsa ya tsinke.

A ajiye acikin akwarin GUMA-GUMA dasu har guda biyar wasu manya manyan duwatse ne kan kura.

.

Cocilar dake hannun insfekta zakari ta kwace ta fada cikin akwatin fus ta fashe ya juyo bakinsa a kafe ya dubi Audu yace Mun dauki adireshin yaran nan kuwa ?

Audu ya girgiza kai cikin kaduwa gami da GODEWA ALLAH DA BA KUDINSA AKA BAWA 'YAR KYAKKYAWAR NAN BA yace.

Bakace mu dauki adireshinsu ba yallabai.

** ** ** **

Washegari misalin karfe hudu da rabi na yamma shafiu yayi fakin da bakar marsandinsa a kofar gidansu aisha zuciyarsa cike da bakin cikin ta leko ta koman da suka gani adaren jiya.
Ga mamakinsa lokacin data fito saiyaga ita ko ajikinta wai an mintsini kakkausa
(ASMA'U MATORI)
domin cikin farin ciki ta tare shi tana murmushi
SANNU DA ZUWA MY ONE.
Shafiu ya dubeta fuskarsa a murtuke yace na fahimce ke Aisha ko jimamin asarar da kikayi bakyayi Aisha ta dube shi gamida girgiza kai daman ba rabona bane shafiu haka allah ya kaddara domin idan abu ya kasance rabonka ne Allah yabaka duk duniya babu wanda ya isa ya hanaka shi haka nan ma idan ba rabonka bane to fa babu wanda ya isa ya baka.
Ina fatan zaka manta da komai musa abinda yake gabanmu acikin zuciyarmu Ta danyi shiru sannan tace babu abinda nake kauna aduniya fiye da kai Shafiu wallahi dukiya dana rasa ajiya bata kai ko rabinka ba agurina Nagodewa Allah da bakaine ka kubuce min ba.
.
Hakan datace shi ya tausasa zuciyar shafiu tayi fari tas don haka ya saki wani fatalwan murmushi yace Haba ai abin ne da ciwo...to amma dai ta bakin naki domin duk dukiyar da zan samu aduniya banza ce idan babu ke Aisha.
Aisha ta lumshe idanu naji dadin abinda ka fada wallahi harkasa zuciyata tayi sanyi.
Yanzu ma ai shiryawa zakiyi mu tafi Aisha ta bude baki cikin mamaki ina zamu?
Mahaifana ne suke son su ganki jiya nabasu labarin ki.
Aisha ta rufe idanu a kunyace tace
'kai haka da wurwuri?
Shafiu ya harareta yace haba aisha shekarata nawa ina kaunar ki? Don Allah je ki shirya kifito mu tafi suna can suna jiran isowarmu.
.
Gani nan zuwa my one ta ruga gida aguje shafiu

yabita da kallo sannan ya girgiza kai cikin murmushi
'Karfe biyar na yamma suka isa gidansu Shafiu aisha ta caba ado da daya daga cikin leshin da shafiu ya saya mata ya kuma sa akayi mata dinkin gaggawa duk da yake duniya ta juyawa mahaifin shafiu baya saida aisha ta rude da ganin yadda aka tsara farfajiyar gidansu shafiu.
Shafiu ya bude mata kofa ta fito sannan sai ya dubeta da murmushi yace zo muje bayan mota nabaki abinda na sayo miki domin ki basu amatsayin kyautarki ta musamman ga iyayena.
Aisha ta rike baki duk duniya banida mai kula dani kamar ka.
Shafiu yayi murmushi sannan cikin farin ciki sai ya zura dan makulli abayan motar domin bude but din motar don ya dauko kyautar.
Yana bude bayan motar sai yayi tsalle gefe guda a tsorace
aisha ta rike kafadarsa a firgice tana duban bayan motar sannan ta karkada fuffuke tace
KUYI HAKURI NA TSORATA KU KO? Ina son ku sano ba nufina na cuce ku ko na tsorata ku ba nazo ne domin na baku dukiyarku da akaso a zalunce ku adaren jiya yau Allah ya nuna min ranar da zan cika alkawarina dana dauka tun tsawon shekara dari da shirin da suka wuce.
Ku leka ku gani dukiyar ku tana bayan motar nasan jiya kwana kukayi bakuyi barci ba kun hadu da azzalumai bata gari ai nayi maganinsu danasa musu GUMA GUMAN DUWATSU ACIKI.
.
Balbela tayi shiru sannan sai ta dubi aisha tace To Aisha sai watarana daga yau bazaki sake ganina ba tana gama fadin haka saita bace.
Shafiu ya dubi aisha murmushi ya subuce masa tun kafin ma ya leka bayan but din motar ya hangi haske da walkiya na tashi aciki.
Jikinsu na rawa suka leka numfashinsu ya dauke cak sa'ar da suka ga but din motar cike da wasu irin kananan duwatse masu kyawun gaske suna haske da walkiya.
.

Dukiyarmu ta dawo aisha shafiu yace sannan yayi tsalle sama ya dire yayi ihu cikin murna ga mamakinsa saiyaga Aisha ba murna takeyi ba maimakon hakan ma sai hawayene ke zuba daga idanunta
Kukan me kuma kikeyi?
Aisha ta goge idanu tace shafiu kada fa ka manta da cewa wannan dukiyar ba hakkinmu bace domin shima kakan nawa..
.
KAKAN NAKI SHIMA ME??
KUDI DA MACIJI - 34
.
KARSHE.
THE END
.
Kukan me kuma kikeyi?
Aisha ta goge idanu tace Shafiu kada fa ka manta da cewa wannan dukiyar ba hakkinmu bace domin shima kakan nawa SATO TA YAYI.
.
Shafiu yaji kamar Aisha ta kwada masa guduma a kirji To yanzu me kike nufi? So kike mu dauki dukiyar aka mu shiga gari neman wanda akayiwa sata shekaru dari da shirin da suka wuce ko me?
.
Ganin ransa ya baci sai Aisha ta matsa kusa dashi ta dafa kafadarsa akaro na farko tace a tausashe Shafiu abinda nake son ka fahimta shine wannan dukiyar ba tamu bace bamuda hakkin taba ta kanaji fa abinda yace shima sato ta yayi.
Shafiu ya dubi asiaha a fusace yace To Idan dukiyar ba tamu bace ta wacece?
Fada min mana aisha dukiyar wacece aduk fadin garin nan?
.
Aisha ta fashe da kuka sannan ta girgiza kai tace WALLAHI NIMA BAN SANI BA.
Shafiu ya matsa kusa da ita yace kada ki sani ciwon zuciya Aishata Yaya Arziki yana binki kina gudunsa ?
.

KARSHE.

.

NAZIR ADAM SALIHI (Nas).

.

KAMMALAWA.

.

Alhamdulillahi
Alhamdulillahi
Alhamdulillahi

.

Dukkan Godiya Yatabbata Ga Allah Madaukakin Sarki Daya Bani Damar Kawo Karshen Wannan Littafi Mai Suna
KUDI DA MACIJI (Maganinsu Kashewa)
Wanda Shahararran Marubucin Nan Wanda Yaga Jiya Yaga Yau Kuma Muke Fatan Yaga Gobe Da Jibi Insha Allah Sannan Jagoran Masu Tsara Rubutun Labaran Fina Finan Hausa Ayanzu.
NAZIR ADAM SALIH